ZEENATU BOOK COMPLETE
Hausa Novels Document
Daga Alƙalamin Boss Bature💋✍️*

ZEENATU💗

Tana a zaune saman swing chair dake a cikin katafaren garden din gidan, fuskarta sam babu walwala sai tarin damuwar da tayi mata katutu acikin zuciyarta, ta yi zurfi cikin tunaninta idanunta suna akan Peacocks din da ke shawagi cikin garden din..

Da matsakaicin gudu motar Alhaji Musa ta kunno kai ta cikin main gate din gidan ta nufo parking space, yana hakimce a backseat din motar idanunsa suka hango mashi ita ta cikin glass window, umarni ya ba drivernsa ya tsaya kusa da ita.

Horn ɗin motar ne ya razanar da ita, a firgice ta ɗago da idanunta da suka kaɗa sukai ja ta dubi motar da a daidai lokacin tayi parking, fitowa yayi daga cikin motar, like always fuskarsa a murtuke ya ɗauki wankan suit.

Ya saba idan ta ganshi da gudu zata nufe shi tayi hugging dinsa amma yau ya sha bamban, tunda ta kalle shi sau ɗaya ta kawar da idanunta gefe ɗaya, hakan ba ƙaramin ɗaga hankalin sa ya yi ba.

Daga gefenta ya zauna tare da ɗaura tafin hannunsa saman kanta ya janyota a hankali ya kwantar da kanta saman kirjin shi, sai lokacin ta samu damar fitar da abunda ke ranta, fashe mashi tayi da kuka.

A ruɗe ya soma shafa bayanta da tafinsa, tare da tambayar ta meke damunta? Wa ya ta6a mashi babynshi? Ko bata jin dadi ne.

Lokaci ɗaya duk yabi ya rude saboda ko kaɗan baya son damuwar Zeenatu.

Cikin shesshekar kuka ta ce, "Daddy, Yaya Shureim.."

"Meya yi maki?"

"Daddy, he stopped paying attention to me bana jin dadin share ni da ya ke yi, I don't know what I did to him, he's completely changed towards me" tun da ta fara magana ya haɗe rai kamar bai ta6a yin dariya ba

"Aunty Benazir ma ta rage kula ni,  ni gaba daya zaman gidan bai yi min daɗi daddy, mommy ma bata da lokaci na, in ta dawo daga office agajiye bata kulani sai ta shige daki ta kama bacci, da anjima kuma in ta farka bata fira da ni, sai dai ta je gurin mommy Layla su yi fira, shima ya Shureim din baya fira da ni da aunty Benazir ya ke yi kullum suna a tare, kaima idan ka tafi sai tsakar dare kake dawowa lokacin na riga da na yi bacci, ni gani nake kamar baku sona, baku damu da ni ba, baku bani kulawa yadda ya kamata..." Ta ƙarashe maganar cikin shesshekar kuka.

Bai ji dadin halin da take a ciki ba, ya fahimci kaɗaici ne ke damun ta, har cikin ranshi bai ji dadi ba.

Shafa sumar kanta yayi cikin sigar lallashi ya ce "Stop thinking that way, my princess, bana so kina sanya damuwa a ranki, you're more important to us than anything, please ki daina fadin ba'a sonki ko ba a damu da ke ba, sanin kan ki ne bani da abu mafi soyuwa da ya wuce ke, ko da kowa zai juya maki baya ki tuna ni ina atare dake, koda bana nan kina a cikin zuciyata..."

kalamai masu tausasa zuciya ya dinga faɗa mata har ya samu ta ɗan lafa da kukan.

Tighting dinta ya yi a kirjinshi ta yi lamo fuskarta sharkaf da hawaye sai faman sauke ajiyar zuciya ta ke yi.

"Daddy yaushe zan cigaba da karatu? Ka ce sai nayi aure zaka barni in cigaba, dan Allah daddy ka yi mini auren, saboda inaso in dinga zuwa makaranta harma in haɗu da ƙawayen da zamu

dinga zumunci atsakanin mu, saboda na fahimci babu tsara na agidan nan shiyasa ba'a zama a yi fira dani...."

Murmushin gefen fuska ya ɗan saki, ya lura da akwai abun da ya 6ata mata rai shiyasa take fadin ta cikin ta.

"Kada ki damu, Nayi maki alkawari ƙarshen shekarar nan, zan aurar dake, kuma zaki cigaba da zuwa makaranta"

Murmushi ta saki saboda taji dadin maganar sa, ba karamin ɗebe mata kewa yayi ba, ya bata lokacin shi sosai sun daɗe suna fira kafin suka sauko daga kan kujerar, hannunsu cikin na juna suka nufi falo.

Lokacin da suka shigo falon, A dining Suka hango mutanan gidan sun hallara suna cin lunch din su, ran Alhaji Musa Ya 6aci ganin yadda su ke yin walwala, hakan yasa shi yarda da maganar Zeenatu, wato basu damu da Zeenatu ta ci abinci ko bata ci ba.

Fusgar hannunta ya yi ya ja ta suka nufi dining din, takun tafiyarsa ne ya ja hankulansu ga duban shi, har saida gabansu ya fadi ganin yadda ya murtuke fuska.

Yana ƙarasowa ya sanya hannu ya damƙi table cloth din da aka shimfiɗa kayan lunch din saman shi, ya hankade shi gaba daya kayan abincin suka 6are kan floor, a sukwane suka miƙe suna kallon shi cikin ruɗu.

A tsorace Zeenatu ta la6e bayansa jikinta na kerma..

Hajiya layla da ranta ya 6aci ta watsa mashi harara tare da cewa, "Wannan wani irin wulakanci ne? Ta ya muna cin abinci zaka 6arar da shi kamar wani ƙaramin yaro.."

Bata ƙare maganar ba ya daka matsa tsawa tare da nuna ta da yatsan shi, "Karki kuskura ki sake min magana idan baso kike in 6ata maki rai ba..."

sakin baki ta yi sototo tana kallon sa, hankalin hajiya Sarah ba karamin tashi ya yi ba, sai yarfa hannayenta take yi tare da marairaice masa fuska don yayi haƙuri.

"Haba Musa, wani irin almubazzaranci ne wannan? Yanzu abun da kayi ka kyauta fisabilillah? Laifin me mu ka yi maka? Meya sa zaka zubar mana da abinci?" Alhaji Ubaid ne ya faɗa cikin fushi,

Harara ya watsa mashi rai a ɓace ya ce, "In har Zeenatu ba zata ji dadi a gidan Ubanta ba, to kuwa babu wanda zai zauna lafiya a cikinku! Saboda rashin hankali kuna nan hankalinku kwance, kun bar min yarinya a waje cikin kaɗaici? Wato baku damu da ita ba, babu ruwanku cikinku kaɗai kuka sani ko!"

Da tsawa ya ƙare maganar kamar zai doke su, Benazir da Shureim sun saki baki suna kallon ikon Allah, sam sun kasa magana..

"Babe, wllh ba haka bane, bansan me Zeenatu ta faɗa maka ba, amma wlh bamu manta da ita ba, ka tambaye su ka ji saida na aika Tani bedroom dinta don ta kira ta tazo ta ci abinci, bayan Tani ta dawo ta ce min Zeenatu tace ba zata ci abinci ba, wai bata jin yunwa, dama kwanan nan fama na ke yi da ita, na rasa gane kanta, da kaina na je ɗakin na matsa mata akan ta zo mu ci abinci amma taƙiya shiyasa na ƙyaleta, na jira saika dawo in sanar da kai..." Harara ya watsa musu, tare da jan dogon tsoki, ya juya yana cika yana batsewa ya nufi part dinsa..

Hajiya layla ji take kamar tabi bayan shi  ta shaƙe shi, saboda haushinshi da ya cikata,

"Wlh Musa bai da mutunci, ni wlh na gaji da wulaƙancin da ya ke yi mana, don kawai muna zaune agidansa...?

Bata ƙare maganar ba, Hajiya Sara ta juya tabi bayan shi, bayan tafiyar ta Shureim da Benazir suka haɗu suna rarrashin mommynsu, Zeenatu dake kallonsu duk tasha jinin jikinta ganin abun da ta ja musu...

Fashewa ta yi da kuka tare da juyawa jikinta na kerma ta nufi hanyar ɗakin ta, bata kaiga ƙarasawa ba Dr. Shureim ya bi bayan ta da sauri ya taso ƙeyarta ya dawo da ita dining din, zaunar da ita ya yi kan kujera ya tsareta da tambayar me ta faɗa ma uncle Musa, cikin shesshekar kuka ta zayyana musu komai, cike da takaici Benazir ta ce, "Haba Zeenatu, me yasa zaki mana haka? Idan mu muka ɓata maki rai why ba zaki faɗa mana ba uhum? Kinsan halin uban naki, yanzu gashi kin ja ya zubar mana da abinci hankalinki ya kwanta ko? Kin shiga tsakanin mu da shi..."

Fashewa ta kuma yi da kuka, Alhaji Ubaid ya ce, "Ya isa haka pls, ni banga laifin Zeenatu ba, gaskiya bakwa kyautawa, ku yakamata ace kuna jan ta a jiki, tunda ku kaɗaine ƴan uwa dake a kusa da ita, bayan haka yarinya ce sai kuna haƙuri da ita.."

Taɓe baki hajiya Layla ta yi, "Ni Zeenatu bata yi mini komai ba, in ita bata da cikakken hankali ai shi uban nata da hankalinshi ko? In ba rashin wayau ba meye na ɗaukar maganar yaro? Ta ƙare maganar tare da jan tsoki ta juya ta bar dining din, da sauri Alhaji Ubaid yabi bayanta don ya lallashe ta.

Cikin shesshekar kuka ta ce, "Am really sorry, idan na ɓata maku rai, ni ban faɗa masa don yayi maku faɗa ba, Aunty benazir am sorry, yaya Shureim kaima ka yafe min.."

Tausayinta ne ya kama su, har su ka ji basu kyauta mata ba, lallashinta su ka koma yi.

"Nasan nine na ɓata maki rai ko?" Ya tambaya yana kallon ta, yamutsa fuska ta yi tare da sunnar da kanta ƙasa,

Kallon Benazir ya yi suka haɗa ido, tashin hankali! gaba ɗaya sun gane inda Zeenatu ta dosa, gashi a halin yanzu Dr Shureim baya jin sonta, tun ranar da Allah ya haɗa shi da Aisha, ya gane ba son aure yake ma Zeenatu ba, rashin Aisha ne yasa har ya kula ta da sunan soyayya, amma a zahirin gaskiya baya jin zai iya haɗa Aisha da wata mace a duniyar nan, bai ma taɓa lura da Zeenatu tayi masa ƙaranta ba sai ranar da idanunsa suka yi mashi tozali da Juliet ɗinsa.

Ƙumshe dariya Benazir tayi, don ta riga da ta gane me ya Shureim ke tunani aransa, ɗan ja gefe ya yi yadda zai kauce ma Zeenatu kada ta ji mi zai ce don yasan zata iya fahimta, cikin harshen larabci ya ce, "Ya zanyi Benazir? Wlh tun da na ga Ummi na ji kamar ancire mini son Zeenatu, yanzu soyayyar da nake mata ta ƴan'uwantaka ce bata aure ba."

Itama cikin harshen larabci ta ce, "Ya shureim sau nawa ina kokarin ankarar da kai akan Zeenatu uhum? Saida na ce maka tayi maka ƙanƙanta, ba sa'ar auranka bace, duk da ba haramun bane don ka yi soyayya da ita, amma ni dama nasan mace ɗaya ce a cikin zuciyarka, ka so zeenatu saboda rashin Aisha, yanzu kuma Aisha ta bayyana, in ka ji zaka iya haɗawa biyun tau, ka dai san Zeenatu da kishi, kuma tsakani da Allah da raini ka haɗa Aisha da Zeenatu yar cikin ta.."

Ta faɗa tana dariya, gaba ɗaya maganganun da suke yi Zeenatun bata fahimtar abun da suke fadi saboda basu ɗaga murya ta sadda kanta ƙasa.

"Ka daure ya Shureim, kada ka karya mata zuciya, ko da ba za ka aureta ba, ka taimaka ka kwantar mata da hankali, wlh tana sonka, kaga ta fara shiga damuwa, in ya so daga baya zamu san abun yi..."

Jinjina mata kai yayi tare da mayar da hankalinsa kan Zeenatu ya matsa wurinta, cikin sanyayyar muryar nan tashi ya ce, "Am really sorry rabin raina, na gane kuskurena, ke ce baki fahimce ni ba Zeenatu, taya zan daina kula abar kaunata uhum?" Murmushi ta ɗan fara saki..

Ruƙo hannunta Benazir tayi a cikin nata, "Pls Zeenatu, ki daina biyewa zuciyarki, wallahi babu abun da ya canza na daga kaunar da mu ke yi maki, mun damu dake, muna son ki rabin ranmu, daga yanzu komai a tare zamu dinga yi in sha Allah, mu ci abinci atare, muyi fira atare, muyi kallo atare, mu yi gym atare, kai har tilawar alqur'ani zamu dinga yi kullum tare da ya Shureim."

Murmushin farin ciki ta saki ga wani dadi da ta ji.

"Yanzu ma ba zamu barki da yunwa ba.." ta faɗa tare da kwala ma Tani kira, jim kaɗan sai gata ta nufo su, tana ganin kayan abincin da aka 6arar a ƙasa ta daura hannu akai tana tambayar meya faru..

"Pls ki kwashe kayan abincin da ya zube ki canza mana wani, sannan ki turo wata maid din ta goge floor din, muna jiran ki."

Benazir ce ta fada, jikin Tani na 6ari ta amsa da toh ta zuƙunna tana tattara kayan abincin, bayan ta gama jera su a tray ta nufi kitchen....

______________UNCLE MUSA

Bayan ya shiga bedroom dinsa yana ƙoƙarin fara rage kayan jikinsa, wayarsa ta ɗau ruri.

zaro ta yayi daga cikin aljihun wandonsa yayi picking tare da kara wayar a kunnansa...

"Sir, har yanzu bamu gano shi ba, a binciken da mu ka yi, ba shi kaɗai ya gudu daga estate din ba, hada yar uwarsa ba'indiyar nan.."

Tsoki ya ja cike da takaici ya ce, "Na raina kokarin ku, tayaya har sakaran mutumin nan ya gagare ku ganowa um!" Ya fada a fusace..

"Sorry Sir, we'll do our best to locate..."

Bai ƙare maganar ba ya daka mashi tsawa yana faman cije le6e ya ce, "Idan har baku gano inda ya 6uya ba nan da one week, ku kuka da kanku! sannan bana buƙatar shi araye da shi da yar uwar ta shi, just kill them all and bury them where no one can find their bodies!"

"An gama sir,"  Rejecting call din ya yi, sai faman fitar da numfashi mai ɗumi ya ke yi, ran manya ya 6aci...

Wani layin ya kira tare da kara wayar a kunnansa,

"Mark, how's his condition? Has he recovered from the coma?"

On the other hand Dr. Mark ya ce "He still hasn't regained consciousness, amma ka kwantar da hankalin ka, yana samun kulawar likitoci, nan bada jimawa ba zai farfado, kasan aminin nasa baya wasa da lafiyar sa"

cije le6ensa yayi tare da jan numfashi ya furzar da shi.

"Ko da zai cire ran shi yaba Omar don ya rayu, bazai ta6a burge ni ba, bana son alaƙar su kwata kwata, sai kace shi na haifa ma shi, Omar ya jima yana baƙanta min rai saboda Owais, shi ya raba ni da shi, ya mallake min ɗa, amma nasan maganinsa dole in shiga tsakaninsu wlh..!"

Bai ƙare maganar ba, ya tsinkayi muryar Hajiya Sarah,

"Babe..."

Nan da nan ya haɗe rai, da sauri ya katse kiran tare da jefa wayar saman mattress, afusace ya juyo yana kallonta tana daga tsaye bakin kofar ɗakin,

"Ban hana ki yi min la6e ba idan ina waya?"

Marairaice masa fuska ta yi, "Am sorry, ba la6e nake yi maka ba, dama na biyo kane don inji meyasa ka yi mana haka pls?"

"Oh! kin biyoni ne don kiyi min faɗa kan abunda na yi halan? Ya fada yana ɗage mata gira..

Ƙwarjini yayi mata hakan yasa ta kasa faɗan ta cikinta..

"In har zaku cigaba da 6ata ma zeenatu rai, nima bazan daina 6ata maku rai ba, yarinya da gidan ubanta ace kowa ya juya mata baya babu mai kula da ita!"

"Bai kamata kana ɗaukar maganar Zeenatu ba, har yanzu fa yarinyace, babu abunda aka yi mata fa, ita ce ta ƙuntata kanta.."

Bata ƙare maganar ba ya katse ta, "Pls, fuce ki bani guri, bana son takura.." gyaɗa kai tayi maganarsa ta 6ata mata rai.

Dama da haushinshi aranta, kwanakin nan kwata kwata baya bata hakkinta yadda ya kamata, in ya fita sai cikin dare ya ke dawowa gidan kamar aljani, tayi ta jiranshi baiwar Allah, har sai bacci ya dauke ta, kuma in ta farka ta gansa ta nemi ya kulata sai ya kama yi mata faɗa yana faɗin ya gaji ita bata da hakuri ne, bata ga a gajiye ya dawo ba, kawai ta kyalesa bacci zaiyi, baiwar Allah zaman hakuri kawai ta ke yi da shi.

"Abincin naka fa?"

"Bazanci ba" Cike da 6acin rai ta ce, "Kada Allah yasa ka ci Musa, ka cigaba da yi min abun da kaga dama, ni da kai in har akwai wanda ke cutar wani Allah zai saka masa ne ka jira ka gani, don kawai ina haƙuri da kai sai ka yi ta min abunda kaga dama..."

A ruɗe yake kallonta cike da mamakin ina ta samu kwarin gwiwar gaya masa magana ido cikin ido batare da jin shakkar shi ba..

"Ƙaddara ce tasa na aure ka, amma wlh nafi ƙarfin ka, koda yake ba laifin ka bane, nina ja ma kaina, shiyasa har ka samu damar wulaƙantani son ranka..."

Juyawa ta yi a fusace ta nufi room door din, batai aune ba taji ya damƙi wuyanta, a tsorace ta kware baki zata fasa ƙara, ya yi hanzarin sanya tafin hannunsa ya toshe bakin nata.

Saitin kunnnanta ya kai bakinsa da wata irin murya mai cike da shu'umanci ya furta, "Matsoraciya..." Ajiyar zuciya ta sauke tana faman haɗiyar yawu...

"Faɗa min a ina kika samu kwarin gwiwar nan ne?" Ya faɗa yana leƙen fuskarta..

"Ka 6ata min rai ne, ni kawai bana jin dadin abun da ka ke yi min ne, basai na fito fili na faɗa maka ba ka riga da ka sani .."

"Am sorry my queen, mother of my princess, na kar6i laifina, bazan ƙara ba, nima bada son raina hakan ke faruwa ba, ayyukane su ke yi min yawa amma zan gyara in sha Allah." ta ɗan yi mamakin yadda yayi mata magana cikin tausasa harshe.

"Muje ki taimaka min in yi wanka, mun kwana biyu bamu yi wanka atare ba.." Bai jira amsarta ba, cikin sigar yaudara da jan hankali ya ɗauketa kamar jinjira ya nufi bathroom da ita.

---

Lokacin da Taj ya je ma Ummi da zancen neman ta da Chief ya ke yi, hankalinta ba ƙaramin tashi yayi ba, zullumi da fargaba suka cika zuciyarta, ta yi ta tunanin meyasa ya ke nemanta?

Kasa fita tayi daga dakinta, har saida Taj ya kirata a waya ya ƙara tunasar da ita game da kiran da Chief ya ke yi mata yace ta same shi yanzun nan a sitting room dinsa tukunna, ta zumbula dogon hijabi ta fito cike da ɗar-ɗar ta nufi sitting room dinsa, saida ta tsaya bakin door din ta daidaita nutsuwarta, kafin tayi sallama cikin nutsastsiyar muryarta.

Daga ciki ya amsa mata sallamar, ya na daga zaune kan sofa ya ɗaura kafarsa ɗaya kan ɗaya yayin da idanunsa ke akan Apple ipad dinsa da ya ke daddanawa, shiga ciki ta yi, tunkan ta ƙaraso ya nuna mata kujerar dake fuskantar sa, table ne ya raba tsakanin su.

Bayan ta zauna ta sunnar da kanta ƙasa cike da jin nauyin sa gaba ɗaya ya yi mata kwarjini.

"Ina fata kin wuni lafiya."

Da ƙyar ta furta, "lafiyalou, ya kake, ya aiki, ya family ɗin ku"

"Alhamdulillah ina lafiya, suma family ɗina suna cikin ƙoshin lafiya,"

Shiru suka ɗan yi na wani lokaci, daga bisani ta tsinkayi muryarsa a cikin kunnanta,

"Na kwaɗaitu da son jin tarihin rayuwarki.."

Zare idanu ta yi, har ta fara tunanin ko dai ya ji komai agurin su Benazir ne.

Bai damu da yanayin ta ba ya ci gaba da maganarsa, still bai ɗago ya kalle ta ba, idanunsa na akan apple ipad dinsa da yake cigaba da dannawa,

"A ranar da ƙawayenki suka zo gidan nan, Taj ya faɗa min halin da kuka shiga lokacin da kuka ga juna, kuma ya ji a bakin Ex-wife din sa cewa ke aminiyarsu ce..."

Har ya ƙarashe maganar bai ɗago ba, yanayin fuskarta ne ya canza zuwa tsantsar 6acin rai da damuwa, kwata-kwata bata son kowa yasan labarinta, saboda tana jin kunyar a sani, bayan haka bata son ta fama tsohon raunin dake a cikin zuciyarta, abun da ya ɗaure mata kai meyasa Chief ya ke son jin labarin ta? Ko Taj da suka fi shaƙuwa da shi bai nemi ya sani ba sai shi da bai ta6a shiga shirgin ta ba hakan yasa ta dan ji shakkun ta faɗa masa..

"Kin yi shiru ba ki ce komai ba,"

Kamar mara gaskiya ta kama yi mashi yan kame kame, muryarta kamar ta mai in'ina ta ce, "Sir, I'm sorry to say why do you want to hear about my life?"

"Saboda ina son in sasanta tsakaninki da ƙawayenki, cos a fahimtana kun samu sa6ani ne, kuma akwai wani abu da ya faru wanda yayi silar raba ku. "

Yamusa fuska tayi kwata kwata babu walwala ta furta, "Ina ganin girmanka yallabai, bana fata Allah ya nuna min ranar da zaka nemi wani abu agurina in kasa yi maka shi, amma ina mai baka haƙuri, ni bazan iya baka labarina ba..."

Gently ya ɗago da reddish eyes dinsa ya ɗaurasu akan fuskarta, tuni ta ji wata nutsuwa ta shige ta, wani irin kwarjini yayi mata wanda hakan yasa ta kasa ƙarasa maganar tata.

"Pls ki faɗamin, In har kin yarda da ni, amma idan kina ganin da takura ki bar shi..."

Yanayin yadda yake yi mata magana cikin kwantar da murya yasa ta dinga jin kamar yaya Shureim ne ke yi mata magana, hatta fuskarsa sai ta dinga koma mata irin ta Shureim, batasan

sa'adda ta fara bashi labarin rayuwarta ba, tiryan tiryan ta labarta masa komai daya faru da ita har izuwa lokacin data bar gidan mahaifin ta.

Idanunta cike tab da ƙwalla ta ƙare maganar, lallashin ta ya yi cikin nuna tausayawarshi gareta har ya samu ya shawo kanta.

"Tayaya akai kika bar ƙasar nan? Ki ka koma America da zama, bayan kin canza rayuwarki?"

Sunnar da kanta ƙasa tayi cike da jin nauyin ta fada.

"Zan fahimce ki Ummi, tun kafin ki fara yi mana aiki mun riga da mun san komai game da rayuwarki a America, don haka kada ki ji komai, abun da ya faru da ke jarabta ce daga Allah..."

Kalamai masu dadi ya faɗa mata har sai da ta ji zata iya fada masa komai saboda ta yaba da hankalinsa ta kuma aminta da shi, a tsanake ta fayyace masa komai da ya faru bayan rabuwarta da mahaifin ta.

Daƙyar ta ƙarasa labarin ganin yadda hankalinsa ya tashi matuƙar sosai, jikinshi har kerma ya ke yi saboda tsabar bacin rai da fusata, bai taɓa jin tsanar mutun kamar yadda ya ji ya tsane sa ba, zaluncin sa yayi yawa, bayan ya rabata da kowa nata, ya kuma maida ta karuwa, cikin fushi ya daki gaban table dinsa da hannunsa.

Hankalinta a tashe ta ce, "Sir meke damunka? Ko labarin dana baka ne baiyi maka dadi ba..!"

"Har yanzu kina atare da Uncle din nata?"

girgiza kai ta yi, "Mun rabu da daɗewa,"

Wani kallo yayi mata da ya sa tasha jinin jikin ta, batasan ya san komai ba.

"Ki ji tsoron Allah, Ki faɗa min gaskiya!"

Tamkar zata fashe da kuka ta ce, "Pls kada ka tilasta mini, bazan iya faɗa maka amsar tambayarka ba, ka yi haƙuri kawai.."

Murmushin takaici ya yi tare da cewa, "Okay, Kin taba haihuwa da shi?"

Aruɗe take kallonsa jin wata tambaya mara ma'ana, ba dan tana ganin girmansa ba da ba abun da zai sa ta zauna yana mata tambayoyi kamar ɗan jarida,

"A'a, amma na ta6a samun cikin shi, wanda silar zubar da cikin da na yi yasa muka samu sa6ani da shi, har ya ɗauke ƙafa da kawo min ziyara, abun da yasa nayi hakan saboda bana so in 6ata shape din jikina sannan bani bukatar in ƙara haihuwa, ƴata dana bari ta ishe ni in ƙarasa rayuwata,  ashe ma ƴar da nake ta hauka akanta ta mutu batare da na sani ba...."

 Fashewa tayi da kuka ya dinga lallashinta har ya samu ta yi shiru..

"Amma meyasa baki taba kar6ar tayinsa na aure ba?"

Tana cikin share ƙwalla ta ce, "Saboda ban ta6a son shi da aure ba, bayan haka a duk lokacin da yayi mini magiya akan in amince in auresa, da zarar na amince muka fara shirye shiryen auranmu toh bazai ƙara lafiya ba, har sai ya fasa zancen auren, wannan dalilinne yasa har ila yau bai aure ni ba."

Duƙar da kanta kasa ta yi jikinta yayi sanyi da ganin yanayinsa, duk sai taji ta muzanta, saboda tayi zaton haushin rayuwarta ya ke ji, tuni idanunta sun cicciko da ƙwalla,

"Kayi hakuri, idan labarin dana baka ya 6ata maka rai, shiyasa tun farko banso ka matsa min akan in fada maka ba.."

A hankali ya buɗe idanunsa da suka kaɗa jawur ya girgiza mata kai, "Ba abunda kike tunani bane Ummi, labarin ki ya karya min zuciyana, na ji tausayin rayuwar ki..." hankalinta ne ya kwanta jin ba abun da ta zata ba ne.

"Nagode da kika aminta da ni har kika faɗa min sirrinki" Ɗan murmushi ta yi.

"Amma kai ma kamar kana da damuwa, kada ka ce na sanya maka ido, wlh ka rame, babu karsashi a jikin ka"

Murmushin yaƙe ya ƙaƙaro akan fuskarsa, "Kada ki damu da ni, zazzabine ke damuna amma na ji sauƙi..." Girgiza kai ta yi, "Yallabai, halin da ka shiga yafi ƙarfin zazzabi, kada ka boye min pls, tun da har na aminta da kai na baka labarina dayake sirrina kaima ya kamata ka sanar dani

taka damuwar, ko da bazan iya sama maka mafita ba, zan tayaka da addu'a." marairaice masa fuska ta yi.

Shiru yayi jim yana tunanin ya zata ɗauki abun in ya fada mata,

Cikin sanyin murya ya ce, "Ummi mun fara gano su wanene Elders na gidan Kurkukun ƙaddara! Kuma muna zargin uncle din ƙawarki Benazir yana ɗaya daga cikin su..."

Bai ƙare maganar ba ganin yadda ta zare idanunta, walwalar fuskarta ta ɗauke tamkar bata taɓa yin dariya ba.

A dabarbarce ta ce, "Sir ka san me ka ke faɗa kuwa? Wallahi ba dan ina ganin girmanka ba da ba abun da zai hana..." Kasa ƙarasawa ta yi, can kuma ta ce, "Bazai yiwu ba, big boss baya ɗaya daga cikin su, saboda shi ba matsafi bane kuma ba mugu bane, ni nasan wanene big boss! Nasan halinsa ciki da bai, pls ku sake bincike akan shi zaka tabbatar da abun da nake faɗa maka!" Rai a ɗan ɓace ta faɗa, ta haƙiƙance akan gaskiyarta.

"Ke baki tunanin mutumin nan da wata mummunar manufa yake atare dake Ummi? Ke fa malama ce, kina da tarin ilimi akan ki, kinsan mai kyau da mara kyau, taya zaki yi tarayya da fasiƙi kuma har kina kare sa daga laifin da ake tuhumarsa...?"

"Baki tunanin saboda kin nuna baki son shi dr. Shureim kikeso shiyasa ya ƙulla makircin da ya shiga tsakanin ki da shureim ya kuma raba ki da mahaifinki saboda yasan bazai bari ki aure shi ba tunda baki son shi, sannan bayan kin gudu da tsakar dare tayaya akai har kika haɗu da shi a wannan lokacin? Shi Aljanine baya bacci ne? Ba yadda za'ayi ya fito in the midst of the night batare da wani ƙwaƙƙwaran dalili ba, gaba ɗaya plan dinsa ne Ummi..."

Shiru tayi jim ba tare data furta kalma ba, bata san tayaya zata fahimtar da Chief ba, gani take kamar ya fara zarewa.

"Kiyi amfani da hankalinki Ummi, meyasa ya ɗauki nauyin karatunku a ƙasar germany? ya kuma kama maku hayar gida, bayan haka duk weekend sai ya kawo maku ziyara har ya kwana agidan ku," ya faɗa yana kallon cikin idanunta.

Gaba ɗaya tabi ta ruɗe, sai dai kwata kwata bata gasgata maganarsa ba, saboda ta yarda da Uncle Musa fiye da kowa tun da ita ya yi mata hallacci, ya so ta a lokacin da kowa ke gudunta, ya zama danginta a lokacin data rasa dangin da zata jingina da su.

Murmushin takaici ya dan saki, saboda ya fahimci ta cikin sauƙi bazata yarda da shi ba,

Zura hannunshi ya yi cikin front pocket na jallabiyarsa ya zaro hotuna,

Kamar daga sama ta ji ya ce, "Nasan har yanzu kuna a tare Ummi, saboda akwai ranar da ya kira ki a waya kin shiga toilet, Batool ta gani ta ɗauka batare da sanin ki ba, a yanzu haka ina da hujjojin da za ki gasgata magana ta.."

She was utterly perplexed, but she didn't believe his words at all.

Ya ƙarashe maganar tare da ɗaura mata hotunan akan table dinsa, lokacin da ta daura idanunta akan hotunan wata irin firgita ta yi, gaba daya tabi ta rude, muryarta da mamaki ta ce, "Sas.. Sir ina ka samu waɗannan hotunan?"

Ta tambaya aƙagare da son jin amsar shi, bai tanka mata ba, har saida ya zaro ɗayan hoton ya jera shi da sauran hotunan..

Lokaci ɗaya ta ƙara ruɗewa, labbanta na kerma ta furta, "Baby preety, Sir Ina ka samu hotunan su um??"

Numfasawa yayi kafin ya ce, "zan faɗa maki inda na samu hotunan amma ki fara faɗa mini miye alaƙar dake atsakanin mutanan dake a cikin hotunan nan?" Jinjina mashi kai tayi kafin ta fara kora masa bayani,

"A tare na san shi da Natasha, sun daɗe a tare, karuwarsa ce kuma baturiyar england ce, ita kuma baby preety rainon ta ya kawo mata tun tana jaririya, amma lokacin da ta kai shekara sha shidda ta ce min ya kar6e ta, ya mayar da ita gurin mamanta da ke anan Nigeria.."

Runtse ido chief Owais yayi saboda takaicin da ya turnuke zuciyarsa, aransa ya ayyana hakan na nufin ƴan biyu ne ita da ƴar wurinsa! Kamar yadda su ka yi tsammani, Ya sadaukar da ɗaya, ita kuma ɗayar tana agurin mamanta.

"Sir meya faru um? Dan Allah tun da na amsa maka tambayarka, nima ka fadamin a ina ka samu hotunan su! Na ƙosa na ji."

Miƙa hannu yayi cikin table drawer din gabansa ya curo diary ɗin Unaizah ya ɗaura mata akan table din, "kinga inda na samu hotunan, Kuma diary din nan mallakin ɗaya daga cikin fursinonin kurkukun kaddara ne, nasan ba zaki manta yarinyar da Unaisah ta bada labarin  mahaifinta da ya yaudareta ya sadaukar ita gidan kurkukun kaddara a matsayin Korean School...?"

Wani irin faduwar gaba taji daram dararam kamar ana buga gangunan yaƙi a ƙirjin ta.

Yatsun hannunta na kerma ta buɗe diary din ta soma karanta shi,

Wa'iyazubilla! tana karantawa yayin da brain dinta ke tariyo mata fuskar yarinyar, tabbas ta yarda diary din mallakin baby preety ne babu tantama saboda yawanci duk abunda ta rubuta a cikinsa ta ta6a jin labarin a bakin Natasha.

Bata ƙarasa karantawa ba, ta rufe diary din tare da kifa kanta saman shi, wlh bazan iya misalta tashin hankalin da ta shiga ba, She was completely bewildered and shocked, unable to believe it, Aranta tana jin ba zai yiwu uncle Musa ya iya aikata rashin imanin nan ba, mutun mai tsoron Allah da tausayi irin sa would never do such terrible thing, amma kuma ta fara kokwanto saboda in har ba a diary din baby preety ba, to kuwa babu inda za'a samu hotunan Big boss da Natasha da kuma na baby preetyn, sai dai bata so ma zargin su akanshi ya zamana gaskiya.

"Yanzu kin yarda da maganata ko kuwa kina akan bakanki"

Jinjina mashi kai ta yi, "Bani da matsaya, amma na yarda da big boss, kuma na yarda da kai, sai dai bazan iya yarda da abun da ka fada akansa ba, wadannan hotunan na yarda a cikin diary din baby preety aka same su amma bana tunanin itace yarinyar da Unaisah ta bamu labarin ta, please na roƙe ka ku sake bincike akan shi.."

Duk yadda Chief ya so ya kwatanta mata cewa ba mutumin kirki bane taƙi yarda, tana akan bakanta saboda ta aminta da mutuminta, yadda kasan wadda aka asirce, kwata kwata bai ji haushinta ba saima tausayinta da ya mamaye zuciyar shi saboda ya lura ta ruɗe ne sosai kuma

bata son zargin da suke yi ya tabbata akan shi saboda halin da zata shiga, shiyasa tun farko baima yi tunanin faɗa mata komai game da babynta ba saboda gudun halin da zata shiga.

"Ummi, Zan baki lokaci kije ki yi tunani akan abun da na faɗa maki, sannan ko da baki yarda ba, Inaso ki bamu hadin kai please..."

Girgiza kai ta yi, "Ka yi haƙuri ba zan iya ba, nayi masa alkawarin bazan ta6a bari wani ya san muna a tare ba, in har ya ji na karya masa alkawari bazai ji dadi ba, zaiga kamar na ci amanarsa ne, ni ko maganarsa bana son yi da wani." Zuciyarsa ta sosu ransa yaso ya 6aci, sai dai bai nuna mata a fuska ba..

"Zaki iya tafiya..." Har zata miƙe ya tsayar da ita, "Zan gargaɗe ki, Kada ki kuskura ki bari mutumin nan ya gane abunda muke zargi akansa! bama shi ba, ko da ƙawar nan taki ce, idan har na ji maganar nan agurin wani, hmm, ba abun da zai hana in garƙame ki a cell kuma kema zaki shiga cikin zargin da muke akan sa, sannan kada ki canza masa ku cigaba kamar yadda kuka sa6a."

Maganarsa ta ɗaga hankalinta, dama da biyu ya yi mata barazana, fuskarta ta jiƙe sharkaf da gumi, kwata kwata babu walwala atare da ita, Ya rudar da ita ba kaɗan ba, Ya kuma tsoratar da ita.

Hanky ya miƙa mata, "Share zufar dake akan fuskarki, don bana so wani ya gane halin da kike a ciki."

Cikin rawar hannu ta kar6i hanky din ta soma share gumin fuskarta, har ce mata yake yi, "Ki share da kyau fa.." tace toh, bayan ta gama ta juya zata tafi da hanky ɗin ya dakatar da ita, "Bani abuna.." miƙa masa hanky din ta yi, ko waiwayensa bata yi ba saboda a ƙagare take da ta bar sitting room din nasa..

Lumshe idanunshi yayi tare da jingina bayan shi jikin kujarar, bawan Allah abun duniya ya ishe shi, saboda gujewa tunanin da zai haifar masa damuwa yasa baya barin zuciyarsa hakanan batare da yayi tasbihi ba 💔

Bayan fitar Ummi daga dakin, jikin bango ta jingina bayanta, yayin da zuciyarta ke tariyo mata wasu abubuwa da suka haifar mata da kokwanto akan mutuminta! bakomai ta fi tunawa ba face

ranar data fara ganin Danish babu shirt a jikinsa! zanen tattoo dinsa ya tsaya mata a rai, har yau bata manta ba, saboda sak irin na big boss ne, kamar anyi photo copy dinsa an ɗaura masa abayansa, kuma tun da take mu'amala da americans bata ta6a ganin mai irin tattoo dinshi ba, sai akan Danish shiyasa ranar data ganshi al'ajabi ya kamata, bayan haka maganganun da Chief ya faɗa a game da shi sun tsaya mata a ƙahon zuciya, tabbas diary din baby preety ne, agurin ta kaɗai za'a samu hotunansu, wani abu da ya ƙara ruɗar da ita nickname dinsa da ta gani a rubuce cikin diary din Preety, kuma a labarin da Unaisah ta basu ta fadi sunan mahaifin Unaizah yar gidan daddy, gaba ɗaya dai kanta ya ɗaure tamau, kwakwalwarta ta rikice sai tufka da warwara ta ke yi.🍁

"Ummi, kun gama magana da Chief dinne?" Cikin kunnanta ta tsinkayi muryar Taj, a firgice ta dube shi yana zaune kan wheelchair dinsa, danne damuwarta ta yi ta kakaro murmushi kan fuskarta, "Eh mun gama magana da shi, shine ma ya ce min in tafi.

Sarai ya lura akwai damuwa atattare da ita sai dai kawai ya basar.

"Yakamata ka ajiye wheelchair din nan, tun da ka fara samun sauƙi, idan ba haka ba zaka manta yadda ake yin tafiya da kafafu," Ta faɗa da zolaya.

Murmushi ya sakar mata, "wlh iya yine irin nawa, kinsan ance sabo turken wawa, ɗan hawan ta da nake yi yasa har na saba da ita.." ya faɗa yana ƙoƙarin mikewa, A hankali ya samu ya tsaya kan kafafunsa, murmushi ta yi mashi, "in shigar maka da kujerar ciki?"

"No, bana so Unaisah tasan na samu lafiya, tafi ji da ni Allah, duk in zata ganni ina gungura kujerar jikinta na 6ari take kamamin ta tura ni.."

Duk da halin damuwar da take aciki hakan bai hana tayi dariya ba, maganarsa ta bata nishadi ashe lambon ciwo yake ma Unaisah.

Bayan ya shiga sitting room din Chief, Jiki asanyaye ta wuce bedroom dinta, tana kallon Unaisah da Batool zaune kan rug, sun baza textbooks dinsu da alama karatu take koyawa Batool, bata bi takansu ba, cikin sanɗa ta wuce don kada su ganta saboda a halin yanzu tafi bukatar kadaici..

~_____💞______💗_____💘_____🌹______💋_____💫_____🫀___~

ISOD HEAD QUARTER AT MEETING ROOM..🔥

Meeting Room ba lafiya, tun da suka hallara, Chief ya zabga tagumi da tafukansa biyu, hakan ba ƙaramin daure musu kai ya yi ba, kiran gaggawa ya sa aka yi musu don su yi meeting, kuma sun zo ya kasa magana ko kallonsu bai yi ba, cike da ruɗu suke ta kallon fuskar sa, daga yanayinsa suka fahimci baya jin dadi ganin yadda ya faɗa, kuma akwai wani abu dake damunsa, duk da sanyin A.c ɗin ɗakin wani irin gumi ne ke keto mashi....Cikin kunnuwanshi ya tsinkayi muryoyinsu sama sama suna yi mashi magana cikin harshen turanci tamkar raɗa,

"Sir Are you Okay?"

"Sir meke damunka? Baka da lafiya ne"?

"Sir pls, gaba ɗaya mun damu da kai, ka faɗa mana in akwai abun da ke damunka.."

Dafa Kafadarsa Commender James yayi, "Owais, meke faruwa da kai ne uhum?"

Sai lokacin ya ja dogon numfashi tare da sauke ajiyar zuciya, a hankali ya zame tafukansa daga kan kuncinsa, ya zube hannayensa saman laptop keyboard din gabansa, a hankali ya ɗago da raunannun idanunsa da suka kaɗa juwar ya bi su da kallo.

Na hannun damansa ne zazzaune kan kujerun dake a gefensa na hagu, daga bangarensa na dama U.s Armies ne tare da General Noah da Taj, wannan karon hada shi Chief ya yi inviting..

"Owais, mun fahimci akwai damuwa atare da kai, daga yanayin ka muka fahimci baka da kwanciyar hankali, Pls, in ba damuwa ka faɗa mana mu nema mafita a tare, mun riga da mun zama ɗaya..." Cikin kulawa General Noah ya yi maganar yana dubansa.

Bawan Allah, kallonsu kawai ya ke yi shi kaɗai yasan meke damunsa, baisan ma tayaya zai fara yi musu bayani ba! Ya za su ɗauki abun idan suka ji cewa kakansa ne Elder! Ya Ilahi, fargaban da ya ke yi kenan shiyasa yake ta jin zullumin ya faɗa abun da ya tara su, abun da takaici.

Numfasawa yayi a hankali ya soma magana,

"Abun da ya sa na tara mu anan, saboda in taya mu murnar cigaban da muka samu a binciken da mu ke yi akan Elders na gidan kurkukun ƙaddara, ina yi maku albishir na gano wanene shugaban kurkukun ƙaddara..." Zare idanu suka yi cike da tsantsar al'ajabi jin abun da ya ce, ya basu mamaki matuka don basu taba zaton nesa zata so musu kusa ba...

"Chef ta yaya akai ka gano Elder? Abun da muke tunanin ba zai samu cikin sauki ba....?" Commender ne ya faɗa da mamaki akan fuskarsa..

General Noah ya ce, "Amma dai ka shammace mu Chief, ka yi matukar bamu mamaki..." Ya faɗa da murmushi akan fuskar.

kwata kwata basu lura da yanayin sa ba, Taj ne kaɗai ya fahimci babu lafiya, aransa ya ayyana zai yi wuya in ba wani nashi ba ne Elder, duba da yadda ya rame ga damuwa tsantsa akan fuskarsa, hakan yasa bai nuna farin cikin sa ba..

"Sir, ba dan daga bakinka na ji maganar nan ba, da sai na ce ba gaskiya bane, saboda na razana da jin ka gano mana tantirin dan ta'addan nan, amma tayaya ka gano sa? Kaina ya kulle, banyi zaton zamu iya gano sa ta cikin sauki ba.." CI ne ya fada..

COO ya ce, "Allah yasa ba mafarki nake ba, Chief pls ka fada mana wanene ɗan iskan mutumin nan uhum? Wani shegen ne? Wlh na ƙosa na ji harna fara tunanin azabtarwar da zamu yi masa, kai mutumin nan ko kotu ba zamu kai shi ba, saboda bana tunanin zasu iya yanke mishi hukuncin da ya dace, mu zamu haɗa baki mu murkushe ɗan iska a cikin cell, But, sir sauran Elders din fa?"

Wani raunanannan kallo ya ke binsu da shi, sai farin ciki suke yi suna ɗurawa Elder ashariya basu san grandpa din sa ba ne, gaba ɗaya sun ƙagara da su ji wanene Elder din sai tambayar shi suke yi yayi shiru yana kallonsu,

Agent Zahra ya ce, "Zan so inga idon azzalumin mutumin nan, ƙarya ta ƙare masa, ko ya zaiji idan muka ɗamke sa, amma kuna tunanin kamasa zaiyi mana sauƙi kuwa? Tun da basa jin makamin mu, zai iya amfani da tsafi ya 6ace..." Ya faɗa da damuwa akan fuskarsa..

A hankali Chief ya dubi Taj dake ta kallonsa, ruwan hawayen da ya gani kwance a cikin idanun Chief ya ɗaga hankalinsa, girgiza mashi kai ya ɗan yi alamar kada ya karaya, cike da damuwa ya yamutsa pink lips dinsa tare da cizon lower lip din da hakoransa.

Cike da rashin kuzari ya miƙe daga kan kujerar da yake ya fuskance su tare da zuba hannayensa cikin aljihun wandonsa, gaba daya suka bi shi da kallo a ƙagare da son jin me zai ce.

Nauyin haɗa idanu da su ya ji, a hankali ya fito daga gaban kujerar ya juya masu baya lamarin ya ɗaure musu kai,

Ya ji zafi aranshi fiye da zafin ƙunar wuta, surutan da suka yi akan kakansa sun ta6a zuciyarsa, ina ga kuma sauran al'umma idan komai ya fallasu, Allah kaɗai yasan cin zarafin da za a yi musu.

Haƙiƙa Baba Obie ya cutar da su, ya ja musu zagi da cin mutunci a idon duniya, sai da ya yi silar ɗaukakar su tukunna ya tarwatsa darajar su..

Gwauran numfashi ya ja, cikin karyayyar murya, mai matukar rauni da ƙarfin hali ya furta, "Ina baku haƙuri da abun da zaku ji daga gare ni, I'm really disappointed, an karya min zuciyata, zallumi da fargaba ne suka hana in sanar da ku tuntuni..."

A ruɗe suke kallon kallon a tsakaninsu, nan take ransu ya fara basu kodai na jininsa ne Elder ɗin? Wataƙil cikin uncles ɗinsa ne, kwata kwata ba su kawo ma ransu zai zama kakansa ko mahaifinsa ba.

"Kada ka ji komai Owais, ka faɗa mana zamu fahimce ka.."

Commender james ne ya faɗa..

Cikin rawar murya ya ce, "Ba mahaifina bane, Ba kuma cikin Uncles ɗina bane, amma wanda ya yi silar zuwan su duniya shine Elder shugaban Kurkukun ƙaddara...."

Tashin hankalin da ba'a saka mashi date, Tunkan ya ƙarasa maganar A kiɗime suka zabura tare da miƙewa tsaye, a lokaci ɗaya suka ɗaura hannayensu saman kawunansu, Idanunsu azazzare cike da tashin hankali haɗi da al'ajabin da ya kamasu! Lamarin ya gigita su.

Duk da sanyin A.c din dake ratsa fatar jikinsu hakan bai hana gumi wanke gaban goshin su ba, wlh sun karaya matuka, Hankalin maza ya tashi.

A sukwane General Noah ya zame hular kakinsa dake a kansa ya kifa ta saman table dinsa..

A dabarbarce Commender James ya furta, "Owais, kana cikin hayyacinka kuwa? Kasan me kake faɗa? Ko ka sha giya ne uhum? Kakanka fa ke nan, Kana nufin Obinna, anya ka yi bincike da kyau? Ta ya ma hakan zai yiwu?"

Girgiza kai CI yayi cike da takaici ya ce, "Sir am sorry to say da wani ne ya faɗamin maganar nan Allah sai ya ci na jaki, Hakan ba zai taɓa yiwuwa ba, ba gaskiya bane, Baba Obie bazai aikata munanan ayyukan nan ba, Owais ka bani mamaki, ban taba zaton zaka iya furta wannan maganar akan kakan ba, kafi mu sanin wanene shi, amma ko mu kanmu da muke abokanka mun yi imanin baba Obie bashi bane Elder, Mutumin mai kyawawan halaye da tausayi irinsa bazai iya aikata abun da Elders suke yi ba...

"Ni dai danasan zaka fada mana wannan almaran da ba abun da zaisa in halarci meeting ɗin nan, sai dai ka yi hakuri Chief amma yau ka ɓata min rai,  ka ce Elder ne kakan ka, Wanda ya haifi baba, gaskiya sir kwakwalwarka bata aiki yadda ya dace kana bukatar a duba ka.." Coo ne ya fada tare da zame glass din kan fuskarsa ya zaro hanky yana sharce gumin dake tsastsafo masa.

Kasa juyowa ya yi ya fuskance su, baisan taya zai yi musu bayani ba, baba Obie ya cuci kansa ya yaudari mutanan da suka yarda da shi, gayanan duk wanda aka faɗamawa sai anyi da gaske kafin ya yarda..

Taj Tuni hawaye sun wanke fuskarsa, dama saida ranshi ya bashi hakan, wata irin karaya ya ji, baba Obie ya bashi mamaki, ba tun yanzu ba ya jima yana al'ajabin dukiyarsa da ɗaukakar ahlinsa ashe bana Allah da Annabi bane, haƙiƙa bai kyauta ma rayuwarsu ba, ya zalunce su wata shari'ar sai A lahira...

"Tun da nake daku na taba yi maku ƙarya? Mutumin nan kakana ne nafi ku sanin wanene shi! Miye ribana in na mashi kazafi? Tun da na ce maku shi ne ku yarda kawai, kakana ne Elder!"

Ya faɗa cikin shesshekar murya ba tare da ya juya ya fuskance su ba,

Wannan karon kusan suman tsaye suka yi saboda sun fara karaya da maganarsa jin kamar yana shesshekar kuka...

"Ba shaye shaye na yi ba, da hankalina da tunanina, Ni ba mahaukaci bane, ba kuma kazafi na yi masa ba, zan sake maimaita maku, Kakana Obinna shine Elder, azzalumin da ya ke azabtar da rayuwar yaran da ba su ji ba basu gani ba a gidan kurkukunsa, mutumin da muke nema ruwa a jallo, ashe daga tsatsonsa na fito, ban ga laifinku ba da kuka kasa yarda da maganata saboda muma lokacin da muka ji hauka ne kaɗai bamu yi ba, na yi fatan ace ban kai wannan lokacin a raye ba, gaba ɗaya mun yi danasanin kasantuwar mu jininsa, amma ba yadda zamu yi haka Allah ya ƙaddara mana, Allah yana fitar da rayyayye daga jikin matacce, Ga misali nan akan mu, Kakanmu gurbatacce ne, mai fuska biyu, mu kuma ba haka muke ba, gaba ɗaya uncles dina da mahaifina babu sa hannunsu a ciki, hasalima basu taba jin wani abu mai suna kurkukun kaddara ba, a ranar da asirin ya tonu, abun ya daure mun kaina, sai na ga kamar ban ma taba sanin shi ba saboda na ji abubuwa game da kakana wanda ni ko iyayenmu babu wanda ya taba sani..."

Jikin taƙaura fa ya yi la'asar, tuni annurin fuskokinsu ya ɗauke duff kamar basu taba dariya ba, zuciyarsu ta karaya, ga baƙin cikin da ya mamaye su, hankalinsu ya tashi, har basu san sa'adda suka cire hulunan kakin da ke akansu suka ɗaɗɗaura su gaban table ba, a ɗimauce suka koma kan kujerun suka zauna tare da sadda kansu ƙasa..

Har tsawon mintuna ashirin cuf babu wanda ya furta kalma daga cikin su saboda matsananciyar damuwar da suka shiga, kwata kwata meeting din yau bai yi musu dadi ba, saboda jin abun da basu taba zata ba, basu ji dadin maganganun da suka faɗa akan kakansa ba, wannan ne karo na biyu da suka ga raunin Chief, ranar da Danish ya faɗa rijiya da kuma yau, wlh sun tausaya masa sosai, sun ma ga kokarinsa da ya iya jurewa in wani ne tuni zuciyarsa zata buga ya mutu ko ya halaka kansa saboda baƙin ciki..💔

Miƙewa Commender ya yi ya nufe shi tare da ruƙo hannunsa ya juyo da shi, hankalinsu ya tashi da ganin siraran hawayen dake zarya kan kuncin sa.

_Zaunar da shi kan kujera Commender ya yi, tare da zaro Hanky ya share mashi ƙwallar shi, mikewa sauran suka yi gaba ɗaya suka kewaye sa duk da raunin da suka yi hakan bai hana su ƙarfafa zuciyarsu gurin lallashin shi da bashi baki akan ƙaddarar data same su, babu wanda bai tofa albarkacin bakinsa ba gurin kwantar masa da hankali, su ka ce ya yi hakuri ya jure radaɗin da ya ke ji, sun san abun da ciwo, dole zai shiga mawuyacin hali amma ya yi hakuri, kada ya ji komai su masu fahimtar shi ne, tabbas su kansu sun karaya sun kuma razana da jin cewa kakansa ne, amma ya zasu yi babu wanda ya isa ya canza abun da Allah ya riga ya kaddara faruwarsa, wlh saboda tausayin da ya basu da suna da halin da zasu cire mashi damuwar shi da ba abun da zai hana su yi hakan kodan su sauƙaƙa mashi radadin da yake ji, amma ba zasu bar shi ba, zasu kasance a tare da shi, No matter what, shi Chief dinsu ne na har abada, su sun yarda da shi fiye da yadda suka yarda da kansu, don haka kada ya ji komai, laifin kakansa ba zai taba shafarsa da ahlinsa ba, zasu tsaya masu tsayin daka don ganin basu tozarta a idon duniya ba, bashi kadai zai yi fadan ba, ya sani yana da su zasu taya shi yin fighting ɗin duk wani wanda yayi yunkurin cin zarafin ahlinsa ta hanyar amfani da abun da kakansa ya aikata! Bayan haka basu san rauninsa, yana ɗaga masu hankali, abun da suke so da shi ya yi ƙoƙarin cire damuwar da ke aransa, saboda zata iya haifar masa da rauni wanda kuma hakan faduwa ne a gare su, sun san Chief ɗinsu jarumin namiji ne, mai dakakkar zuciya, kuma mai tawakkali, basu so ya canza daga yadda ya ke a da, ya sawa ransa cewa zai iya, ya manta da cewa kakansa ne Elder, ta haka ne zai kore damuwarsa har su samu su ƙarasa aikin su."_

Maganganu masu daɗi da ƙarfafa gwiwa suka gaggaya masa har saida
ya ji karfi a jikin shi, sun faranta ranshi, kuma dama abun da ya kamata kenan idan mutun ya shiga wani hali a tausaya masa, a ja shi a jiki, bawai a dinga cuzguna masa ba saboda wata ƙaddara ta same shi, wasu har daɗi suke ji su dinga bullying ɗinka don su baƙanta maka rai, su ja depression ya kama mutun daga haka har ya lahanta kan shi, wa'iyazubilla..💔

Tun suna share mashi ƙwallar da ke gangarowa kan kuncinsa har ta kai ga sun fara tsokanar shi, baisan sa'adda ya fara sakin murmushi ba, saboda dadin da ya ji har godiya ya yi musu, su ka ce kada ya damu hakkinsu ne su bashi kulawa, yanzu tunda sun fahimci ba ya jin dadi yana bukatar ya ga likita saboda lafiyarsa, don haka zasu ɗaga meeting din, zuwa lokacin da zai ji sauƙi.

Ya ce masu bai ƙi shawarar su ba, amma bazai yiwu a ɗage meeting ba, akwai muhimman abubuwan da yakamata su tattauna akai idan ba haka ba zasu iya fuskantar matsala, hankalinsu ya tashi da jin hakan, suka ce tun da haka ne, zasu tafi hutun awa uku saboda sun damu da lafiyarsa suna so ya huta...

A cikin yan mintuna suka kira lsod docs suka bincika lafiyarsa anan cikin medical room ɗin su, bayan sun tabbatar da ciwon dake damunsa ya gargaɗe su akan kada su faɗa musu sakamakon saboda baya son kowa ya sani...

Lokacin da suka koma zaman meeting din, ba laifi sun ga ya ɗan saki jikinshi da walwala akan fuskarsa, A tsanake ya fayyace musu komai da ya faru bayan zuwan Khala..

Sun yi matukar mamakin jin cewa kakarsa ce, kuma Obie ne ya yi ƙaryar mutuwarta ya kai ta kurkukun kaddara, duk ba wannan ba, abun da ya basu haushi da takaici abun da Pravin ya aikata, ashe shima Elder ne na gidan kurkukun kaddara, lallai Obie Family sun haɗa giggan ƴan ta'adda acikin su.

Bayan sun taya shi murnar ganin grandma ɗinsa, da jimamin abun da ya faru da familyn sa Commender James ya ce,

"Yanzu ta ya za'ai mu iya gano sauran Elders? Kana ganin grandma ɗinka zata iya samun sauƙi nan kusa!" Girgiza kai ya yi, "Bakowa ta sani a cikin su ba, yanzu haka da ita da aunt ɗin nawa an ƙwantar da su asibiti basu san inda kansu yake ba, amma suna samun kulawar likita.."

"Me zai hana mu tuntubi shi Elde...Au, afwan sir grandpa nake so na ce,..." murmushi chief ya yi tare da kallon CI da ya yi maganar. "Duk yadda ma ka faɗa daidai ne CI, already na yi masa magana akan ya fada mun sauran Elders din amma ya ƙi sanar da ni...." Nan ya labarta musu abun da suka tattauna tsakaninshi da baba Obie.

Kallon kallo suka jefawa junan su cike da tashin hankali, Agent Jabeer Osman ya ce, "Akwai sauran rina a kaba kenan, In har bamu yi gaggawar kamasu ba zasu iya mayar da hannun agogo baya, nasan iwar haka suna nan suna shirin kawo mana farmaki."

Gaba ɗaya sunyi amanna da maganarsa, Agent Zahra ya ce, "Ni damuwana ina zasu farmaka? ya tambaya yana duban su,

"Hankalina ya fi karkata akan fursinonin da muka baro a Csh."

Taj ya ce,"Asibitin yana da tsaro tunda na sojoji ne, amma fa kada mu dogara da hakan, mun riga da mun san su wanene Evil Giants, in har suka farmake mu da su, toh Allah ne kaɗai zai iya ƙwatar mu, za su iya amfani da sihiri su kashe sojojin dake tsaron su, su kwashe yaran abunda ba a fata, amma menene mafita...?"

gaba ɗaya suka zurfafa tunaninsu kowa na tunanin abun da yakamata a yi.

"Kuskuren da muka yi tun farko shine barin makaman da grandma ta bamu, da mun sani mun taho da su, saboda da su kaɗai ne za'a iya yaƙar su.."

A cewar Captain..

Cike da takaici Canal ya daki gaban table dinsa yama rasa abun cewa..

Jackson ya ce,"Akwai gagarumar matsala, dole fa mu fara kai masu farmaki kafin su kawo mana idan ba haka ba, ba zasu yi mana da dadi ba, bamu san ina zasu farmaka ba!"

Lieutenant Thompson ya ce, "Ni dai a nawa ganin shawara ɗaya ce, Chief grandpa shine mafita, shi kaɗaine makamin da muke da shi a yanzu, tun da ya ce zai mika wuya toh ya taimaka ya faɗa mana komai idan ba haka ba, ba zamu iya cin galaba a kansu ba, a kowani lokaci zasu iya kawo mana farmakin bazata..."

Girgiza kai Chief Owais ya yi, "mu yi hakuri mu nemi wata mafitar, saboda ba irin magiyar da ban yi masa ba amma ya ƙi fada mun, ya ce a dokar aikinsu wani baya tona asirin wani, alkawari ne suka ɗaukarwa junansu, kuma shi ba zai ci amanarsu ba, tun da har ya fadi hakan bai duba ƙaunar da yake yi mini ba, toh wlh ba zai taɓa bamu hadin kai ba, koda zamu azabtar da shi ne, amma a maganarsa ya ce in har aka kawo mana farmaki mu sanar da shi, amma wannan ba mafita bane, tayaya za a yi mu san za'a kawo mana farmakin?"

Da damuwa ya jefa musu tambayar, gaba daya sun shiga tashin hankali..

"Ni a ganina mu fara nemo wadanda grandma ta fadi sunayen su? In ya so sai muci ubansu mu azabtar da su har sai sun faɗa mana su wanene sauran Elders din..." Taj ne ya fada yana huci zuciya ta kai wuya..!

General Noah ya ce, "No ba zamu iya kama su ba, har yanzu bamu da isassun hujjojin yin hakan!"

"Sir, muna da isassun hujjojin da zamu iya kama su..."

Gaba ɗaya suka maida hankali akan Taj da ya yi maganar har suna haɗa baki gurin tambayar wata hujja ce? Bai jira Chief ya bashi umarnin ya faɗa ba, ya fara zayyana musu komai da ya faru tun daga kan labarin Ummi har izuwa labarin da Benazir ta bashi akan Alhaji Musa.

Lamarin ya ɗaure musu kai, basu gama shan mamaki ba, sai da Chief ya samu ƙwarin giwar tunawa da wata hujjar da yake da ita, nan shima ya labarta musu komai da ya gano game da shi tun daga kan hotansa dake a cikin diary din Unaizah, ya ƙara da cewa, "Har yanzu bai rabu da Ummi ba, bayan ya rabata da kowa nata ya maidata karuwarsa, shine ya tafi da ita America..." A rude U.s armies suke jefawa junansu kallo mai cike da tsantsar al'jabi, Ummi dai da suka sani tantiriyar karuwa yau sun ji asalin labarinta da kuma azzulumin da ya yi silar canza rayuwarta, gaba ɗaya basu ji dadɪn abun daya faru da ita ba, tausayinta ne tsantsa a kan fuskokinsu, ba su kaɗai ba hatta General Noah dana hannun daman Chief sun nuna tausayawar su a gare ta, labarinta ya taba zukatansu, kuma basu taba ganin mugun mutun irin Musa ba, labarin yarinyar da ya sa su zubda ƙwalla ashe shine Ubanta, sun ma riga da sun yanke ma kansu shine JAN WUYA mutumin da suke nema ruwa a jallo..

Chief Owais bai dakata ba, ya ɗaura da basu labarin da Sheikh Imam ya ba shi ...

Taj ya ce, "dama sai da raina ya bani, sune suka kashe Uzair..." Ya faɗa cikin ƙunci da baƙin ciki.

General Noah ya ce, "Wai ni Musan nan bashi bane former president ba? Mahaifin Ddg? Kuma ƙanwarsa tana auran daddynka ko?" Jinjina mashi kai Taj ya yi.

Cikin fushi Noah ya buga saman table rai a 6ace ya ce, "Babu tantama zai aika, Ni dama bai ta6a burgeni ba, mutun sai girman kai da izza ashe dukiyar tasa ta kungiyar asiri ce, shi dama karen yan siyasar nan na daɗe ina zargin sa saboda mugun munafuki ne.."

CI ya ce, "Zai yi wuya in ba daga tsatson fir'auna ya fito ba, mutun ba imani ba tausayi!  Zalunci da muguntа kaɗai yasa gaba, aikuwa dubunsa ta cika, daƙiƙin kwata kwata baya amfani da kwakwalwarsa, gashi nan cikin rashin sani ya tabka kuskuren da ya yi silar tonuwar asirin sa..."

 Coo ya ce, "Wlh ikon Allah ne, ka duba yadda ya daɗe yana sheƙe ayarsa tsawon lokaci batare da an iya kamasa ba, wai a haka har matsayin president ya taka, ko da yake ya samu ɗaurin gindi ne..." Bai ƙare maganar ba, Taj ya yi masa gyaran murya tare da furta "Hattara dai.." Cike da jin kunyar Chief CI ya sunnar da kansa, bawan Allah Chief ɗan murmushi ya saki tare da ɗan girgiza kan kanshi.

"Sir, Yanzu meye abun yi tunda muna da isassun hujjojin da zamu iya kama su? Taj ne ya faɗa yana dubansu..

Commender James ya ce, "Babu bukatar 6ata lokaci, mu kama su kawai su fara kar6ar sakamakon zunubin da suka aikata..."

General Noah ya ce, "da shi ɗan iyan, da Musan, da pravin da aminnan grandpa, da likitocin da momma ta faɗa suna da sanya hannu suma a kama su, sannan kada a kuskura abar pravin ya ƙetare kasar nan, nasan  iwarhaka yana neman hanyar da zai gudu, watakil ma ya gudun, shiyasa banso kuka ɗauki lokaci baku sanar damu ba, wlh da kun faɗa mana tun ranar da abun ya faru zamu bi diddiginsa mu kama ɗan iskan, amma na yi maka uziri nasan alhinine ya hana ka sanar mana..."

Chief ya ce, "Mun tattauna da Uncles dina, suma zasu bada gudummuwarsu..." Nan ya labarta masu abunda suka tattauna da Uncles ɗinsu, sunji dadi kuma sun ƙara jin kwarin gwiwa a tare da su..

"Bayan haka tun ranar da ya gudu nake ta trying layinsa a kashe yake, har jaraba bin diddiginsa na yi amma ban iya gano komai ba, ina tunanin ya jefar da wayar ne don kada mu bi diddiginsa."

Agent Zahra ya ce, "Zai iya yiwuwa ya canza layi, in kuwa yayi kuskuren zuwa yin register zamu iya samun bayanansa."

"Ita yar'uwar tashi ka kira layinta ne?"  James ne ya tambaya..

"A ɗaki tabar wayar, na kar6i number dinta a hannun yan uwanta maids, dana kira sai na gano location din wayar a cikin gidan ya ke, da kaina na shiga na dudduba dakin har na gano wayar nata."

Taj ya ce, "Za mu iya haɗa baki da abokan aikin nata, ita Hajjatyn zata iya yin kuskuren kiran wani daga cikin su tun da ta yarda da su atare suke aiki, ko basu ba mu nemi aminiyarta ta ƙut da ƙut, wadda muke da tabbacin zata iya kiran ta, sannan mu haɗa baki da ita, da zarar ta kira ta tayi hanzarin sanar damu, mu kuma sai muyi kokarin bin diddigin su..." Shawarar da Taj ya kawo ta yi masu daɗi..

Ya kuma cewa, "Amma ni abun da ya ɗaure mun kai, Ita hajjatyn tasan abun da ya aikata kuma ta bi shi suka gudu? Ko dai dama a tare suke aikata 6arna ta bayan fage..."

Amma da kamar wuya saboda Hajjaty mutuniyar kirki ce .." Wani marayan kallo Chief ya yi masa..

"Mugu bashi da kama Taj, abun da ya faru da ni ya isa yasa ka dauki darasi, ba kowani nagari bane mutumin kirki, akwai masu fuska biyu, a fili Musa a zuci fir'auna, ni bana zargin ta, amma ta aikata babban kuskure da ta haura ƙafa ta bi shi suka gudu, in har muka gano da sa hannunta akan abun da ya faru da auntyna, kuma tasan abunda yake aikatawa wlh na lahira sai ya fi ta jin daɗi, dole mu hukuntata daidai da abun da ta aikata, babu wanda zamu ragamawa kamar yadda bazan raga ma kakana ba, dole kowan nan su ya gir6i abun da ya shuka..."

Ya faɗa tare da bugun kan table din gaban su, gaba daya idanunsu akan fuskarsa, maganarsa ta burge su, suna alfahari da shi, ya cancanci su yaba mashi saboda jajircewar shi akan gaskiya, a dai yadda duniyar nan ta baci da rashin son gaskiya, da wani mai son kan ne idan yasan nashi ne yake aikatawa 6oyewa zai yi, ko ya bashi hadin kai ya gudu don kada a kama sa, ko kada su kunyata a idon duniya, gaskiya samun mutun mai irin zuciyar chief zai yi wuya a fadin duniyar nan, he's a true leader, ba karamun mai tsoron Allah bane zai yi hakan💘💋...

Almost one hour suna tattauna yadda zasu kama Elders, kowa yana kawo idea dinsa, a karshe suka yanke shawarar zasu tuntubi Ummi saboda ta hanyar ta ne suke sa ran za su damƙi Musa ta cikin sauƙi. Chief ya ce su bar komai a hannunshi ya riga da ya yi mata magana amincewarta ya ke jira, zai ƙara yin magana da ita duk yadda su kai zai sanar da su..🔥

*PRAVIN❗*

Aje Motarsa yayi a haraban wani gida, fitowa yayi jikinsa sanye da suit ya rufe fuskarsa da mask, hatta hannayensa da ƙafafunsa ya saka musu safa, sai yan waige waige ya ke yi daga gani yana a cikin fargaba, zagayawa yayi ta baya ya buɗe boot din motar, ya janyo ƙaton buhun dake a ciki ya aje ƙasa, kafin ya bude backseat ya sungumo baƙar jakarsa ya rataya ta kan kafaɗarsa, da sauri ya ja buhun ya shige da shi ciki, kulle door din ya yi da code kafin ya nufi Ciki.

Shigarshi falo keda wuya ya soma jiyo kakarin aman da ta ke yi, hankalinsa a tashe ya zame jakar ya jefar kan sofa ya saki buhun cikin sauri ya nufi bedrom din da take.

Yana shiga ciki bai same ta a saman gadon ba, sai dai bargonta dake a yashe ƙasa, cike da fargaba ya bangaje kofar toilet ya shiga yana haki saboda gudun da ya yi, lokacin idanunsa suka sauka akan ta yayin da take a gaban sink tana kwarara amai tamkar yan hanjin cikinta zasu zazzago, ta daddafe bakin sink din da hannayen ta.

Ƙarasawa ya yi da sauri ya dafe kafadarta yana yi mata sannu. Bata ko kula shi ba sai da ta gama amayar da komai da ta ci, ta kunna faucet ruwa ya wanke aman.

Kokarin daukarta ya yi don ya sauwaƙe mata tafiyar, cikin bacin rai ta bangaje shi ya yi taga taga zai faɗi yai saurin tsayar da kansa yana kallon ta.

Tsantsar bacin rai ne akan fuskarta, idanunta sun kumbura sun kaɗa jawur saboda kukan da take sha, gown din dake a jikin ta tayi squeezing kamar an ƙwatoto daga bakin kura, doguwar sumar kanta ta cukuikuye kamar ta mahaukaciya, mace mai tsafta ta zama ƙazamar karfi da yaji saboda rashin lafiya da damuwa..

A hankali zafafan hawaye suka soma zarya kan kuncin ta, labbanta sun bushe ƙamas sun ɗan faffashe ga jikin nata har yanzu ba sauƙi..

Cike da bacin rai ta furta, "Karka kuskura ka ƙara matsowa kusa da ni, i don't want to see you Pravin, ka nisanta kanka dani, idan ba haka ba zan yi ma kaina illa!" Bai ta6a ganin Hajjaty a cikin fushi irin na yau ba..

A hankali ya sanya hannu ya cire mask din dake akan fuskarsa, cikin yan kwanakin nan saboda zullumi da fargaba har rama ya yi, tun ranar da ya gudo da Hajjaty, bai nufi ko'ina ba sai guest house dinsa da ya daɗe da mallakarsa, babu wanda yasan yana da gidan.

"Ba halin ki bane, bansan ki da fushi ba, na rasa gane kanki cikin kwanakin nan, duk abun da kika ga ina yi saboda in kare ki ne, amma kin kasa fahimta na.."

Harara ta watsa mashi, cikin bacin rai ta ce, "Idan ba halina bane to kai ne ka sauyani Pravin, ni bazan cigaba da yarda da munafuki ba, na gaji da sauraran ƙarairayin ka! ka faɗa min gaskiyar abun da ya faru, ka raba ni da mutanan da nake rayuwa da su ka kawo ni wani gida ka boye ni a cikin sa! Kullum na tambaye ka sai ka yi shiru, wai me ka ɗauke ni ne? Don ina da hakuri ba hakan yana nufin bani da hankali ba! Zan iya jure komai amma wallahi bazan jure rainin wayon ka ba...."

Tuni ya sha jinin jikinshi jin yadda Hajjaty ke masa faɗa kamar uwarsa, tana magana tana ciccije le6enta saboda radadin da take ji..

"Tayaya kake tunanin zan cigaba da zama da kai? Bayan baka ɗauki iyalinka da muhimmanci ba sai ni Pravin? Wani laifi ka aikata ne da yasa har ka gudo da ni? A ranar kafin in fita hayyacina na ji muryar Hajiya Saratu a cikin kunnena, ta shigo daki na, duk da ban ji abun da ku ka tattauna ba amma raina ya bani ta gano abun da muke yi shiyasa har ta shigo ɗakina, kuma na ji lokacin da ta bangaje mu muka faɗi daga nan ban ƙara sanin inda kaina yake ba..."

Dakatawa ta dan yi tana jan numfashi idanunta a cikin na shi, ya yi zuru zuru ya rasa ta ya zai shawo kanta, kwanakin nan basu jituwa saboda yaƙi faɗa mata laifin da ya aikata, ta ƙi kwantar da hankalinta balle har ta ji sauƙin abun da ke damunta..

Girgiza kai ta yi idanunta suka cicciko da ƙwalla...

"Ka kasa kare kanka saboda baka da gaskiya shiyasa ka yi shiru ko? Ni ina ji araina wani laifi ka aikata musu shiyasa ka gudu da ni, saboda hujjar daka bani bata gamsar da ni ba.."

Sunnar da kanshi kasa ya yi, jikin shi ya yi sanyi lakwas, baisan ya zai yi ba, ya jefa rayuwarsu a cikin bala'e da masifa, ya yi danasani tafi sau a ƙirga, yana matukar jin kunyar Hajjaty, yana jin nauyin tasan miyagun laifukan da ya aikata wa'iyazubillah!!

Bata ƙara yin magana ba, ta juya ta nufi kofar fita da sauri ya bi bayanta, shigowa cikin dakin ta yi, jikinta na kerma ta nufi bedside drawer ta soma kwashe magungunanta tana jefa su cikin dustbin din dakin, shigowa ya yi da sauri ya damƙi hannayenta, kokoyi suka kama yi..

"Pls ki saurare ni, zanyi maki bayani, ki daina zubar da maganinki, da tsada na siye su saboda lafiyarki..."

Wani kallo ta wurga masa, "Ban damu ba Pravin, bana son lafiyar tawa, nafi son na mutu, saboda wanda na yarda da shi yana neman ya karya min zuciyata..."

Bai san sa'adda hawaye suka wanke fuskar shi ba, duk yadda ya so ya dakatar da ita abun ya ci tura, ƙarfi yasa gurin ɗaukarta ɗungurugum ya kwantar da ita kan gadon, ta dinga kuka tana

bubbuga mattress da hannayenta, bin ta ya yi saman gadon ya janyota jikinshi tana turjewa, ya rungume ta kan ƙirjin shi, duk yadda ta kai ga jin haushin shi da ya yi mata hakan sai da ta ji sassaucin damuwarta.

Cikin sanyin murya ta ce, "Pravin dan Allah ka fadamin meyasa ka gudu da ni? Meyasa ka bar Obie estate? Wani laifi ka aikata? Kada ka yi min karya Pravin, babu sirri atsakanin mu, kasan bani da kowa in ba kai ba, kaine majinginata, ƙashin bayana, bana so ka ci amanar yardar da na yi maka Pravin, dan Allah ka faɗamin na yi maka alkawarin zan rufa maka asiri kuma zan taya ka neman mafita.."

wani irin tsantsar sonta da tausayinta ne ya mamaye zuciyar shi, tsoma yatsun hannayensa ya yi a cikin sumar ta yadinga cakuɗa gashinta kamar yana mata susa,

Cikin sanyin murya ya ce, "Ki yi hakuri na boye maki ne saboda bana so na ɗaga maki hankali, amma gaskiyar abun da ya faru, Hajiya Saratu ta gano ina zuwa dakin ki, harma in kwana, bayan mun dawo an fara shirye shiryen family meeting, sai na shiga ɗakinta don in canza kayan dake a jikina, ina kokarin cire riga na jiyo muryarta a cikin toilet tana yin waya ƙasa ƙasa kamar bata so aji, saina lallaba na je bakin ƙofar dakin na yi mata la6e

a nan na ji tana faɗin wallahi bazata sa6u ba, dama ta jima tana zargin kin asirce mata miji saboda yadda kike gayu, wallahi ba zata ƙyale ki ba, sai ta kashe ki da poison..."

 Zare ido Hajjaty ta yi,

Pravin ya sha mur ya ci gaba da zabga mata ƙarya, "Da na ji haka gabana na faduwa na fara tunanin me yakamata in yi saboda nasan mugun halinta na kishi wlh tsaf zata kashe ki, ni banma san wani munafukin bane ya kulla maki makirci, na so inji da wa ta ke yin wayar, ina jin alamun ta gama yin wayar na ma fasa canza kayan, jiki na na kerma na baro dakin nata, na nufo ɗakin ki don in faɗa maki abunda ke faruwa, shigowata keda wuya ina kokarin in tashe ki na ganki a kudundune cikin bargo, kwatsam na jiyo muryar hajiya Saratu daga waje tana tambayar maids ina ne ɗakin ki? da sauri na la6e bayan labule ina jira inga me za ta yi maki, tana shigowa ɗakin ta nufi gadonki hannunta ruƙe da poison..."

Dafe kirji Hajjaty ta yi jikinta ya hau 6ari, daɗi ya ji acikin ranshi ganin ta fara yarda da maganarshi..

"Ji nayi bazan iya bari ta cutar dake ba saboda nasan ba imani gare ta ba, saboda tashin hankali banma san lokacin dana yi wuff na fito daga bayan labulen ba tana jin motsi na ta juyo mu ka yi ido biyu, ta ware baki zata fasa ƙara na shaƙeta tana ta sambatu tana faɗin maciya amana, zarginta ya tabbata akanmu, wlh saita kashe mu, da na ga ta turje ta ƙi saurarena kawai saina sumar da ita, na sungumeki na bar estate ɗin da ke, don nasan muddin ta farka kwanan mu ya ƙare..."

Cike da damuwa Hajjaty ta ce, "Banji dadi ba, amma koma wanene ya ƙulla mana makirci Allah ya isa tsakanin mu da shi, mutane basu tsaron Allah. Amma hajiya Saratu bai kamata tana daukar zigar wani ba, ko da ya ke dama ta tsaneni, tasha faɗamin saita raba ni da gidan ubanta, amma bansan tsanar da ta yi mini ta kai har haka ba, kuma dama kwanaki ko hanya bata son haɗawa da ni, abinci ma indai ni na dafa bata cin shi.."

Pravin ya ce, "Hmmm, ɗan adam fa ba abun yarda bane, indai ka biyewa mutane zasu kaika su baro ka, kuma dama bata sonki ta sha saka ki kuka, ta ƙuntata maki saboda tana jin haushin zaman da kike yi agidansu, ni kaina da nake mijinta bata ƙyaleni ba,  kullum saita goranta mini saboda ina zaune gidan ubanta. Saratu bata da wayau, sakarya ce, kwata kwata bata da halin kirki, zaman hakuri kawai nake yi da ita, amma ni kaina ba sona ta ke yi ba, wahalar da ni ta ke yi, taita juyani son ranta." Yana magana yana yamutsa fuska,

"Amma pravin meya kamata mu yi yanzu? Ni ina ga kawai mu je mu basu haƙuri mu faɗa masu gaskiya, In ba haka ba za su mana kallon mutanan banza kuma maciya amana.."

Waro idanunsa ya yi, "Ke! Kina hauka? Tab lallai, ay wlh muddin muka koma estate din nan sai sun hukunta mu, sai ka ce kin manta irin yadda baba Obie da yayyanta suke ji da ita?

"Pravin, koma me zai faru mu ne masu laifi, mutanan nan sun yi mana hallaci, sun yarda da mu, tsawon shekara da shekaru muna rayuwa acikin su basu taɓa gudun mu ba, amma mu muka ƙi fada masu alaƙar dake atsakaninmu, bamu kyauta ba, kuma nasan zasu fahimce mu in har mu ka je muka basu haƙuri muka kuma faɗa masu akwai aure a tsakanin mu za su yafe mana, koda hajiya Saratun bata yarda ba nasan za su yi ƙoƙarin sasanta mu da ita, tun da su din mutanan kirki ne suna da hankali da kuma tausayi...."

Bata ƙare maganar ba ya tari numfashinta da cewa, "Hmmm, na lura har yanzu baki san halin hajiya Saratu ba, nasan mutanan kirki ne amma wlh akan Saratu zasu iya komai, kin manta labarin dana baki lokacin da ta zo da ni don inga danginta? Ƙiri ƙiri suka nuna basu sona sun tsaneni saboda ni ba jinsin su bane, kuma bani da asali da arziki irin nasu, a lokacin ba don baba Obie ya goya mini baya ba ai da basu bani auranta ba..."

Dafe kai ta yi da hannu ɗaya, "Me zai hana mu tuntuɓi baban toh? nasan zai taimaka."

"Har yanzu kin ƙi fahimtata, nifa bazan ci gaba da zama ƙasar nan ba, saboda hajiya Saratu ba zata raga mana ba, ƙwara mu tattara yanamu yanamu mu tafi, don yanzu haka nemanmu suke yi ruwa ajallo don su hukunta mu.."

Maganarsa ta ɗaga hankalinta, da damuwa ta ce, "Pravin meya kawo maganar barin ƙasa? Ka san me kake faɗa kuwa? Ina zaka kai ƴa'ƴan naka da matarka? kaima kasan wannan bamai yiwu bane, kawai saboda asirinmu ya tonu sai mu gudu kamar waɗanda suka aikata wani mugun laifi...?"

dafe kanshi yayi da hannu ɗaya baisan tayaya zai shawo kanta ba..

"Pravin ka daina wannan maganar, ba zan ta6a baka shawarar ka tafi ka bar iyalinka ba, bamu aikata laifin daya kai har mu gudu ba, kawai kuskuren mu shine ƙarya da muka yi masu tun farko muka boye masu gaskiya, in har muka nemi yafiyarsu bayan mun faɗa musu komai wlh zasu yafe mana Pravin, mun shaƙu da mutanan nan, mun saba da zama cikinsu, sun zama kamar danginmu da muka rasa! Sun ɗauki nauyin komai namu Pravin, wlh idan muka gudu baza su ji dadi ba, zasu ga kamar dama da wata manufa muke atare da su shiyasa bayan mun samu abun da muke so muka tafi, kai baka tunanin halin da ƴa'ƴanka da matarka za su shiga? Wai kuwa Pravin anya kana jin kanka amatsayin ubansu..."

bata ƙare magabar ba ya toshe mata bakinta da yatsan shi..

Ta rasa meyasa take ji aranta kamar pravin ba gaskiya ya fada mata ba! Saboda yanayinsa da kuma maganganunsa abun tuhuma ne! Kawai saboda ƙaramin laifin da bai kai ya kawo ba sai ya gudu ya bar iyalinsa?

Ganin kamar ta fara ɗago shi ya sa shi saurin daidaita nutsuwarshi cikin sanyin murya ya ce, "Na gane kuskurena,  kawai bana so ta cutar dake ne shiyasa na yi wannan maganar, amma ba har cikin raina ba, ni ba zan iya tafiya na bar iyalina ba, banma san na fada ba, ki yi haƙuri idan na 6ata maki rai.." Ajiyar zuciya ta sauke, "Yanzu da yaushe zamu je estate din mu nemi yafiyarsu?"

"Me zai hana mu bari sai an kwana biyu, lokacin da suka yi kewarmu, koma suka neme mu da kansu don su ji ba'asi sai mu je mu faɗa masu gaskiya,..."

 ta aminta da maganarsa saboda a halin yanzu tasan jiran su suke yi.

"Na yarda, amma tayaya zasu neme mu? Bayan babu waya gaba ɗaya mun barsu agidan.."

Yamutsa fuska ya yi, "Kash, sam na manta, amma akwai waya da na siya, nama yi mana hada siyayyar kayan abinci, da duk wani abu da zamu bukata.."

"Pravin basu da layin da zasu tuntubemu a yanzu."

"Karki damu, ki bari da kaina zan je estate din, in faɗa masu komai in sun hakura suka yafe mana zan sanar da ke komai." Ta ce, "Toh Pravin, yaushe zaka je ne?" A takure ya yamutsa fuska, kwata kwata bai son tana yi masa maganar Obie estate, da tasan masifar da suke a ciki da bata ƙara marmarin ambaton ko da sunan estate din ba.

"Ƙarshen satin nan." Ajiyar zuciya ta sauke, "Toh Allah ya kai mu, amma dan Allah ka kwantar da hankalinka, bana so in gan ka a cikin damuwa, addu'a yakamata mu yi Allah ya sa abun ya zo da sauki su yafe mana." Jinjina mata kai ya yi batare da ya furta kalma ba. Ta yi tunanin hajiya Saratu ce damuwar shi batasan mugun abun da ya aikata ba.

Ruƙo hannunta ya yi, "Mu je in taimaka maki ki yi wanka, yau kwana huɗu jikinki baiga ruwa ba." Bata musa mashi ba ya ɗauke ta kamar jinjira ya nufi toilet da ita, after mins ya futo dauke da ita, ta yi ɗaurin ƙirji da towel, ya kwantar da ita kan gadon shi.

Juyawa ya yi ya nufi closet tabi bayanshi da kallo tana mai ƙara jin kaunarsa saboda kulawar da ya ke bata.

Dawowa ya yi hannunsa ruke da riga da wando na shan iska, tun ranar da ya kawota nan ya siya masu kaya kala uku uku..

"Za ki iya sakawa ko in taimaka maki?"

Murmushi ta sakar mashi, "Bana so kana wahala, na lura hada damuwar ciwona ke damunka, kada ka damu zan ji sauki in sha Allah..." Murmushin yaƙe ya yi mata..

Bayan ta karɓi kayan ya fuce daga ɗakin, shiru bai dawo ba, saukowa ta yi daga kan gadon, bayan ta kammala zura kayan a jikin ta, ta je gaban mirror tana kallon kanta.

Zuciyarta cike fal da kewar Ahlin Obie, ita dai ta kamu da ƙaunarsu tun farko, kuma ba ta jin zata iya rabuwa da su ko da hajiya Saratu zata hukunta su ne, ta ji zata zuƙunna kan gwiwowinta ta roƙeta akan tayi hakuri ta yafe su.

Bakomai tafi ji ba face halin da ƴa'Ƴansu za su shiga idan suka rabu.

Can kuma ta canza akalar tunanin nata, ta fi jin kewar aminiyarta akan komai, ta so ace akwai waya a hannunta da ba abun da zai hana ta kira Turai ta faɗa mata halin da suke a ciki tasan zata fahimce su kuma zata taimaka masu..

Body oil ta shafa ma skin dinta ta dauko comb ta sharce gashin kanta dakyar dakyar saboda yawanshi ga tauri da ya yi ga kuma jikinta ba ƙwari..

Jin shiru pravin bai leƙo ba ya sa tayi tunanin ko ya fita daga gidan ne.

Hakan ya sa ta miƙe daga gaban madubin ta fito ta shiga falo, ɗan madaidaici ne ya haɗu sosai, Pravin ya daɗe yana kokarin jan hankalinta da ta dawo gidansa da zama ta ƙiya saboda bata son rabuwa da obie estate...

Idanunta ne suka hango mata bag ɗinsa da ya ajiye kan sofa, sakamakon jefar da ita da ya yi lokacin da ya shigo har ta buɗe abubuwan dake a ciki sun zubo waje..

Buhun ta nufa ta soma buɗe shi, ba komai ne a ciki ba face kayan abinci, komai da zasu buƙata ya siya masu, murmushi ta yi  tare da miƙewa har zata juya idanunta suka sauka akan passports dake ajiye kan hannun kujera.

Zuwa ta yi gaban kujerar, ta kai hannu ta curo Passport din da ta gani, shiru ta yi jim tana duddubasu aranta ta ayyana me Pravin zai yi da passports dinsu?

Bata kawo komai ba a ranta ta mayar da su cikin jakar ta yi zipping dinta, ƙamshin suya ta fara juyowa a cikin hancinta, murmushi ne ya bayyana akan fuskarta jin motsin shi

Direction din da take jiyo motsin ta nufa, dadi kamar zai kashe ta ganin pravin yana girka mata abinci, daga shi sai short a jikin shi, ya haɗa gumi sai aikin motsa suya yake yi...

Kamshin naman ne ya daki hancin ta, cikin sanda ta shiga ciki ba tare da sanin shi ba saboda ya bata baya.

Hugging dinsa tayi ta baya, wata firgita da ya yi saida ta yi noticing wani abu,

"Waw.. waye...! " Ya faɗa tare da ɗaga ƙaton spoon din hannunsa da niyyar ya kwaɗe wanda ya ruke sa..

Ajiyar zuciya ya sauke ganin Hajjaty ce,

"meyasa baki yi min sallama ba?"

"Saboda in baka tsoro." Ta faɗa da murmushi..

"Hmm, zan rama ne Allah."

"Ki koma daki pls, har yanzu babu ƙoshin lafiya atare dake, idan na gama zan kawo maki a daki."

Maƙe mashi kafaɗa ta yi, "Kaima kasan bazan bari kana yin aikin da ya kamata ace ni zanyi ba, in har ba zaka bari in taya ka ba, to ka bani in ƙarasa tun da jikin nawa da sauki."

Dakyar ya lallabata har ya samu ta koma falon ta zauna.

Bada jimawa ba ya fito hannunshi ruke da tray, daga saman shi plates ne na chicken pepper soup, da na shinkafa, ga juice a glasses.." Tunkan ya karasa ta fara haɗiyar yawu..

A saman rug ya a je tray ɗin ta sauko ta zauna shima ya zauna suka tasa tray din a tsakiyar su..

A tare suke ciyar da juna, idan ta bashi a baki shima sai ya bata...

Suna ci suna fira, duk ta ishe shi da santi..

"Da ka yi mini girkin nan har ka tuna min lokacin da muke a gida, kafin mu yi aure, ni dai na yi dacen ɗan uwa kuma yayana sannan mijina, tun ina ƙaramata kake kula da ni baka ta6a gajiyawa ba, ci na, suturata, da duk wata ɗawainiyana kaine,  baka ta6a bari na da yunwa ba, koda kai zaka rasa toh zaka nema min ni in ci..." Idanunta cike tab da ƙwalla ta yi maganar.

Jikinsa ya yi sanyi lakwas.

_"Dan Allah Pravin no matter what, kada ka canza daga yadda na sanka, ka ji tsoron Allah ka kuma kiyaye sa6a masa, da ka zalunci wani ƙwara kai azalunce ka saboda Allah baya yafe hakkin dake a tsakanin bawa da bawa, ka kau da ido ga abun da ba halal dinka ba, ka yi haƙuri da abun da Allah ya baka. Duk abun da ka samu shine rabonka, ita duniyar nan ba matabbata bace, wata rana zamu mutu mu barta ne, lahira ita ce matabbata kuma dawwamammiya, mu ruƙa tuna mutuwa da kwanciyar ƙabari, daga kai sai halinka za a binne ka, komai da muka tara anan zamu bar shi, kowa zai girbi abun da ya shuka, walau na alkhairi ko na sharri...."_

Tun da ta fara yi masa nasihar jikinsa ya soma 6ari, zuciyarsa ta ƙuntata sosai. Bai ƙarasa sauraronta ba ya miƙe kamar zorarre ya nufi daki, yana shiga ya faɗa kan gadonsa ta rubda ciki ya kwanta..

Da gudu ta bi bayan shi, ta hau kan gadon tana tambayar shi me ya faru? Meke damun shi? Ko nasihar da ta yi masa ne bata yi mashi dadi ba...

Cikin karyayyar murya ya ce baya jin daɗin zuciyar shi bacci yake so ya yi,  saukkowa ta yi daga kan gadon taje gaban mirror ta dauko tissue box, yago tissue din ta yi, ta koma kan gadon ta soma goge masa hannayensa da bai wanke ba, bayan ta gama ta daura box din saman drawer..

Rungume kanshi a ƙirjinta ta yi, tana jin yadda zuciyarsa ke harbawa fat fat kamar zata tsaga ƙirjinshi. Ta ruɗe da ganin yadda ya razana daga kawai ta yi masa nasiha, sai dai bata kawo komai aranta ba, a haka bacci ya yi awon gaba da su.

Luxury-incense By Sapnah Borno.
Ta kawo muku turarukan wutan su Na maiduguri dana chad, turarukanta masu masifar dadi da kama waje harma da daukar hankali, indai kikayi kabbasa da turaren ta har wajen da kika zauna indai kika tashi sai kin bar kamshin ki, sannan Tana saida mayukan gashi irin nasu na shuwa Arab masu tasirin gaske, wajen gyaran Amare kuwa babu magana dan tazo muku da Chadian and Sudanese dilka Wanda zaki gyara jikinki da kanki, oga ya kasa ganeki, haka zalika akwai wata humrar ta mai suna hana bacci da kuma sirrin shuwa Abun ba magana, yar uwata ki

jarraba turaren yar mutan borno nasan zata zame miki best turaren wuta plug. Tanada turarukan da zaki turara gida, toilet, bedsheets, curtains, kabbasa and hair incense ku jarraba kada ku bari ayi babu ku.
Wardrobe balls
Kabbasa spray
Chadian khumra
Hawee
Halud
Gabgab
Sandal sukkariya
Kajinguru
Dilka soap
Ready to use dilka
Karkar oil
Turaren tsuguno
Habil
Dorut
Dorot after period
Brown khumra
Dufr khumra
Body milk
Sudanese kuleccam
Chadian dufr kuleccam
Musk khumrah.

Maganin matan mu sunada inganci Wanda muke kawo su daga sudan, sannan munada maganin karin girman nono, Wanda basuda effects, ga masu bukatar maganin Matsi ko maganin mata Masu aiki garanti munada su, sannan muna zuwa gyaran jikin amarya a duk garin da take

Our Chadian aphrodisiacs are.
Beejay fire
Sata jagab honey
Wetness and sweetness combo
Daka
Great A sabaya
Breast engagement powder
Ciccibi
Gumbar madara
Gumbar dabino
Bita Zaizai

08093772168

*Welcome, Littafin kurkukun ƙaddara 500 ne, dukanshi Book One two and 3 Idan kin shirya biya ga Details da zaki tura*

3196407426

First bank

Bature Hafsat Muhammad,

*bayan kin tura zaki bada transaction reciept ko screenshot na debit alert a matsayin shaida ta wannan number din 08103884440*

~_____💞______💗_____💘_____🌹______💋_____💫_____🫀___✍️~

Luxury-incense By Sapnah Borno.
Ta kawo muku turarukan wutan su Na maiduguri dana chad, turarukanta masu masifar dadi da kama waje harma da daukar hankali, indai kikayi kabbasa da turaren ta har wajen da kika zauna indai kika tashi sai kin bar kamshin ki, sannan Tana saida mayukan gashi irin nasu na shuwa Arab masu tasirin gaske, wajen gyaran Amare kuwa babu magana dan tazo muku da Chadian and Sudanese dilka Wanda zaki gyara jikinki da kanki, oga ya kasa ganeki, haka zalika akwai wata humrar ta mai suna hana bacci da kuma sirrin shuwa Abun ba magana, yar uwata ki jarraba turaren yar mutan borno nasan zata zame miki best turaren wuta plug. Tanada turarukan da zaki turara gida, toilet, bedsheets, curtains, kabbasa and hair incense ku jarraba kada ku bari ayi babu ku.
Wardrobe balls
Kabbasa spray
Chadian khumra
Hawee
Halud
Gabgab
Sandal sukkariya
Kajinguru
Dilka soap
Ready to use dilka
Karkar oil
Turaren tsuguno
Habil
Dorut
Dorot after period
Brown khumra

Dufr khumra
Body milk
Sudanese kuleccam
Chadian dufr kuleccam
Musk khumrah.

Maganin matan mu sunada inganci Wanda muke kawo su daga sudan, sannan munada maganin karin girman nono, Wanda basuda effects, ga masu bukatar maganin Matsi ko maganin mata Masu aiki garanti munada su, sannan muna zuwa gyaran jikin amarya a duk garin da take

Our Chadian aphrodisiacs are.
Beejay fire
Sata jagab honey
Wetness and sweetness combo
Daka
Great A sabaya
Breast engagement powder
Ciccibi
Gumbar madara
Gumbar dabino
Bita Zaizai

08093772168.

~___________________________________🍁🍁🍁~

*Me ya Faru Bayan shigar Sheikh Imam Malik*?

Ko sallama bai yi ba saboda 6acin ran da ya ke ciki, dakatawa ya yi yana tunanin meyasa Taj ya kira shi a irin wannan lokacin? Menene dalilin kiran nasa? Me kuma ya kawo Alhaji Ubaid da iyalinsa gidan?"

Yasan dai ba su da wata alaƙa da Chief Owais, zuciyarsa ce ta raya mashi ko dai sun kira sa ne saboda sun ji komai da ya faru tsakaninsa da ƴarsa, shiyasa suka kira su Alhaji Ubaid don su sasanta su.

Ƙunci ne ya mamaye shi, har ya juya zai fuce ya tsinkayi muryarta mai tattare da sautin kuka a cikin kunnanshi..

"Baba! Dan Allah kada ka tafi, ni nasa ya kira mini kai saboda ina son ganin ka, ina bukatarka a kusa da ni, ina so na yi magana da kai..."

Jin muryar gudan jininsa ya sa shi dakatawa da yin tafiya, ya manta when last ya ji muryar ƴarsa yayin da take kiran shi da sunan babanta.

Ganin bai da niyar juyowa ne yasa ta nufe shi tana kuka ta zube saman gwiwowinta a bayan shi, ta rurruƙe ƙafafunsa da hannayenta da ke kerma.

Ba zai iya misalta yanayin da ya shiga ba, ya ji wani irin abu da ba zai iya kwatanta shi ba, sam ya kasa magana.

Shesshekar kukan Aisha ya kashe mashi jiki, ya kuma fama masa raunin dake a cikin zuciyar shi, shekara goma sha takwas rabon da jikinsa ya haɗu dana gudan jininsa, ƴarsa ɗaya tilo da ya kora daga gidansa tare da jinjira a tsakar dare ba tare da ya yi tunanin wani hannu zasu faɗa ba, akan laifin da bata ji ba bata gani ba, wanda har yau idan ya tuna yana jin baƙin ciki mara misaltuwa.

Dakyar ta iya miƙewa ta rungume shi ta baya, tare da kwantar da kanta saman kafadarsa ta zagayo da hannayenta saman cikin shi.

Duk yadda zuciyarta ta kai ga tafarfasa da baƙin ciki sai da ta ji sanyi ya ratsa ta, jin ɗumin mahaifinta a jikin ta.

Hannayenta da ta ƙanƙame cikinsa da su ya bi da kallo, sai ya rinka tuna ranar da mahaifiyarta ta haife masa ita, ta damƙa masa amanarta tana atsaka da fuskantar ajalinta, hakika ya ci amanar malama Batool.

Hawayen da suka cika idanunsa ne suka fara zarya kan kuncinsa.

"Baba! meyasa baka ta6a nemana ba, tsawon shekara goma sha takwas, bakasan irin rayuwar da na yi ba, hankalinka a kwance ka ke gudanar da rayuwar ka, baka ta6a tunanin wani hali nake a ciki ba, ina lafiya ko bana lafiya, ina raye ko bana raye, duk da abun da ka yi min hakan bai hana zuciyata tunanin ka ba, kullum ina sa ran zaka neme ni, amma shiru har sai da na fidda rai da ina da uba a duniyar nan, ka yi min iyaka da kowa nawa, baba hankalinka a kwance kake rayuwarka bayan ƴarka ɗaya tilo da kake da ita tana rayuwa a wani wurin, ko har yanzu fushi ka ke da ni? Baba ka ta6a danasanin abun da ka yi mini? Ka kuwa san halin da kasa na jefa rayuwata?"

Maganganunta sun karya zuciyar shi, duk yadda ya kaiga jurewa saida kuka ya kubce masa, jikinsa na kerma ya ruko hannunta tare da zagayo da ita, ya rungume ta akan ƙirjinsa da hannayensa biyu ya tallabe bayanta.

Komai dake faruwa akan idanun Alhaji Ubaid da iyalinsa, haka zalika akan idanun Abie da iyalinsa, da kuma Taj wanda ke a tsaye gefe ɗaya.

Idanun kowan nan su ya cika tab da ƙwalla saboda tsantsar tausayin Aisha da mahaifinta, kamar sun samu tv haka suke ta kallon su.

Cikin shesshekar kuka da rauni ya furta, "Ki yafe mini Aisha, hakkinki ne ke bibiyar rayuwata, na ci amanar mahaifiyarki, na cuce ki na kuma cuci kaina..."

ya ɗan dakata yana mayar da numfashi, fuskarsa har kerma ta ke yi.

Daƙyar ya ɗaura da cewa, "Taya zan guji gudan jinina kuma in zauna lafiya? Allah shine shaidata, wallahi na yi danasani tun a daren ranar dana kore ki na gane kuskure na, bansan meyasa nayi maki haka ba Aisha! Bana a cikin hayyacina Aisha, bayin kaina bane, ina tsaka da bacci na farka da tsanarki a zuciyata, na ji kin fita araina, kawai bana son ganin ki, kamar ana tunzura ni, a lokacin ji nake in har ban kore ki ba zan iya rasa raina, na daɗe ina tambayar kaina meyasa na yanke maki ɗanyen hukunci! Bayan nafi kowa sanin wacece ƴata, Aisha, bazan iya

misalta maki mawuyacin halin da na shiga ba bayan dana neme ki na rasa, na yi kukan da ban ta6a ƴinsa ba arayuwata, na tsani kaina, na ƙuntata rayuwata, na ji rayuwar duniyar ma ta sire mini, mutuwa nakes o kawai na yi, Aisha gidan mahaukata ne kawai ban je ba, amma na yi haukan rashin ki, har kulle kaina na yi tsawon kwanaki ba asan inda nake ba ba ci ba sha, na yi rashin lafiyar data yi silar kwantar da ni asibiti, na yi jinya kamar bazan rayu ba, bansan wa ke akaina ba, saida ta kai ga sunanki kaɗai nake fada a cikin sambatuna, Aisha yanzu haka da nake maki magana ina da ciwon zuciya, Allah ne bai ƙaddara zan mutu ba, shiyasa na kawo har wannan lokacin a raye..."

Shesshekar kukan Benazir da Anila ne ya cika kunnuwan kowan nan su.

"Aisha ban manta dake ba, da ke nake kwana da ke na ke tashi araina, addu'ar da nake maki kullum a cikin sallata ban daina ba, kamar yadda ki ke sa ran zan neme ki nima haka nayi ta sa ran wata rana zaki dawo ki neme ni, amma baki ta6a tunanin kiyi hakan ba, shiyasa zuciyata ta karaya na yi tunanin ko kin mutu ne ko kuwa abun da na yi maki ne yasa baki ta6a nema ba..." Ya ɗan dakata yana mayar da numfashi.

"Bani da kwanciyar hankali saboda zullumi da fargaban a wani hali kike a ciki, kullum saina kira layinki amma ban ta6a samun shi a kunne ba, kuma ban fidda rai ba, kullum addu'ata idan kina a raye keda jinjirarki Allah ya kare mun ku a duk inda ku ke, Ya zama gatan ku, Ya kuma haɗa ni da ku, idan kuma baku a raye Allah Ya jikanku da rahamarsa, ban ta6a gajiyawa ba da neman ku, saboda ku na sha zuwa aikin hajji don in yi maku addu'a..."

Kasa karasa maganar ya yi saboda raunin da zuciyarshi ta yi, baiwar Allah ta yi kuka kamar ranta zai fita, bata taba tunanin ya damu da ita har hakan ba, ta yi zaton yana sane ya yi watsi da ita shiyasa bata ta6a tunanin ta dawo gida ba tun da bai neme ta ba, ta yi zaton har yanzu fushi ya ke yi da ita.

Tallabo fuskarta ya yi da tafukan sa, idanunsu da ke tsiyayar da kwalla suka haɗu cikin na juna.

"Aisha, saboda ke na ajiye aikina na rabu da kowa nawa, a karshe ma da na yi jiran shiru baki dawo ba, sai na bar ƙasar ba tare da sanin kowa ba."

Numfasawa ya yi tare da girgiza kansa cike da danasani ya daura da cewa, "A ranar dana fara ganin ki a gidan nan, wani irin farin ciki mara misaltuwa na ji, kamar anyi min albishir da gidan aljanna, saboda na ji daɗin ganinki da ranki da lafiyarki, duk da na shiga tashin hankali saboda

sauyin da na gani a tare dake, daga yanayin shigarki, na gane kin canza hali, har saida na yi kokwanton anya Aisha nane?"

Amma saboda jinina dake yawo a jikinki yasa ban musa ba, a lokacin dalilin da yasa ban yi ma ki magana ba, saboda ina jin kunyarki, kema kuma sai kika nuna kamar baki taba sanina ba, shiyasa jikina ya yi sanyi, amma bayan na koma gida saboda farin ciki ban iya runtsawa ba, kwana na yi ina nafilfili don nuna godiyata ga Allah da ya bayyanar min da ke, har so nake Chief ya gayyace ni don in zo gidan nan saboda kawai zumudin in ganki.. "

komai saida Imam ya fayyace mata na daga halin da ya shiga bayan rabuwar shi da ita.

Bai ƙare maganar ba, Ya saki fuskarta da ya tallabe, ya tattare ƙasan jallabiyar Jikin shi da niyar ya zuƙunna kan gwiwowinsa don ya nemi yafiyar ta.

Lura da hakan yasa ta yi saurin ƙanƙame shi tana rokonshi akan kada ya zuƙunna mata, ya bari, kada ya yi, idan ma akwai wanda ya cancanta ya nemi yafiyar wani atsakanin su toh ita yakamata ta nemi yafiyar sa, yana kuka ya ce mata ta barshi ya zukunna, idan har baiyi hakan ba bazai ta6a yafe ma kansa ba, koda ta yafe masa, saboda ya dade yana yi ma kanshi kallon mugun Uba, mara imani, saboda rashin adalcin da bai yi mata ba.
Ta fashe da wani sabon kukan ta ce, "Baba babu yafiya atsakanin mu, abun da ya faru bayin kanka bane, haka zalika abun da ya faru tsakanina da yaya Shureim bayin kan shi bane, a yau na ji komai baba. Na ji abun da ya ɗaga hankalina ya kuma karya zuciyata, Baba ashe dama makirci ne aka kulla min saboda a ɗauki fansa akanka?"

Kaitsaye maganar ta ratsa kunnuwansu, a ruɗe suke kallonta.

Muryarsa na rawa ya furta, "Bangane me kike nufi ba? ki yi min bayani yadda zan fahimta!"

Gajiya ta yi da tsayuwa, hakan yasa ta zauna shima ya zauna yana fuskantarta, yayin da sauran mutanan dake a falon suke atsaitsaye babu alamun gajiya a tare da su.

"Ke nake sauraro Aisha.." A ƙagare da son ji duk da yana fargaban abun da ya daɗe yana zargi ya zamana gaskiya.

"Baba, zan faɗa maka, amma zan roke ka, dan Allah ka yi min alkawarin zaka jure komai da za ka ji daga gare ni, kuma duk abun da zan faɗa maka ya riga da ya wuce, kuma anyi ne don a cusa maka baƙin cikin da zai yi silar mutuwarka, sannan kuma a lalata martabarka da ƙimarka, in har ka tada hankalinka akan abun da za ka ji toh zai yi nasara ne, shiyasa bana so ka sanya

damuwa a ranka, nasan za ka ji raɗaɗin da yafi na ƙunar wuta zafi a cikin zuciyarka amma ina so ka tuna komai ya faru a rayuwar mu mukaddari ne daga Allah, ka ɗauki hakan a matsayin jarabawa da Allah ke yiwa bayinSa muminai, mu yi hakuri da cutarwar da aka yi mana, In sha Allah zamu ga ribar hakurin da muka yi, kuma Allah zai yi mana sakayya"

Cikin sanyin murya ta ƙarasa maganar tana kallon fuskar mahaifin nata dake kallonta da rinannun idanunsa.

Unexpectected ta ji ya furta, "Musa!"

kowa da ke a falon sai da gabansa ya faɗi da jin sunan da ya ambata.

Ba ta yi mamakin Jin ya canki sunan shi ba, dama tasan dole ya zo masa a rai tun da shine babban maƙiyinsa a duniyar nan.

"Ki faɗamin shine ko? Shine ya shiga tsakanina da ke ko?" Cike da damuwa ya tambaya,

Fargaban amsa mashi ta ke yi saboda zullum halin da zai shiga, tasan mahaifin nata da zuciya komai zai iya faruwa.

Daƙyar ta jinjina mashi kai cikin raunanniyar murya ta ce, "Shine baba, uncle Musa, ya daɗe yana ƙulla makirci atsakanin mu, ban taɓa ganin azzalumin mutun irinsa ba, ya karya mini zuciyata, ya ha'ince mu, wata shari'ar sai a lahira, amma ya cutar da rayuwar mu..."

kamar a mafarki suke sauraron maganar Aisha, gaba daya sun kasa tantance wani Musan take magana akan shi, Taj ne kaɗai ya san komai, sai kuma Benazir da Anila.

Sauran da ke a falon sun ruɗe sosai, sun rasa gane inda ta dosa.

"Aisha kada ki ji komai, ki fadamin kawai, bazan karaya ba, nasan zai aikata saboda ya kullace ni a ranshi, dama ni saida na yi zargin dasa hannunsa a cikin abun da ya faru,  kawai don bani da hujjar da zan tuhume sa ne.."

ya faɗa cikin karfin hali kamar zai iya jurewa.

Ƙarasa shiga cikin falon suka yi, saboda su samu damar jin komai, a saman sofas kowan nan su ya samu wuri ya zauna suka nutsu suna kallon Aisha da baba Imam, kwata kwata basu san da zaman su ba, saboda hankalinsu ba akansu yake ba, basu san ma sun shigo falon ba.

Numfasawa tayi cikin karyayyar murya ta soma zayyana masa komai da Uncle Musa ya faɗa mata, tiryan tiryan abu ɗaya da ta boye masa saboda gudun halin da zai shiga, shine karuwancin da ta yi a America da kuma haramtacciyar alaƙarta da Musa tasan in ya ji wannan komai zai iya faruwa ita kuma ba ta so Musa yayi nasara akan mahaifinta, ta dai sakaya ta ce shi ya kaita America ya ɗauki nauyin komai nata saboda ya kawar da tunaninta akan dawowa gida.

Tunkan ta ƙarasa labarta mashi Hajiya Layla ta miƙe tsaye tana tafa hannayenta a kiɗime take zabga salati, Alhaji Ubaid dake a zaune sai jinjina kansa ya ke yi yama kasa furta komai saboda ƙuncin da zuciyarshi ta yi mashi, ina ga Dr shureim dake neman zaucewa saboda tashin hankalin da ya haifar masa da raɗaɗi mara misaltuwa a zuciyarsa, bai taɓa zaton Uncle musa zai iya yi masa haka ba, saboda yasan shi ya cutar da rayuwarshi shiyasa ya dawo da shi gidan shi da zama, haka lokacin da ya ke neman taimako yaita kiransa baya shiga ashe blocking ɗinsa ya yi, kowa dake falon sai da ya razana ba kaɗan ba, Musa ya karya zuciyoyinsu, basu taɓa tunanin shine munafukin da ke ƙulla musu makirci ba.

Saboda bacin rai da fusata yasa shekh Imam zubda gumi akan fuskarsa, ba a taɓa cin galaba akanshi ba sai wannan karon, Musa ya cuce shi, wani laifi ya yi masa da yasa shi yanke masa mummunan hukuncin nan?"

Kawai saboda ya hana shi auran Aisha? Saboda baƙin zalunci da rashin imani ya shiga tsakaninta da shi, yayi mata kazafi bayan ya shiga tsakaninta da Shureim, abun da yafi bakanta ransa tsawon shekarun da ya raba shi da ɣarshi, ashe yana a tare da ita, saboda zalunci irin na shi, yanzu ya gane komai da ya faru da Aisha shi ya ja mata, tun da akan shi yake ɗaukar fansa, bata ji ba bata gani ba. Ruƙo hannayenta ya yi a cikin nashi, saboda kerma da jikinshi ke yi itama nata jikin ya kama kerma idanunsu a cikin na juna yana kuka tana kuka ya ce, "Allah Ya yi maki sakayya Aisha, Allah ya bi maki hakkin ki. Wlh bamu ya cuta ba kanshi ya cuta, la'ananne, In sha Allah sai rayuwarsa ta wulaƙanta tun a gidan duniya, na yi danasanin sanin shi a rayuwata, dama wasu mutanan Allah yana hadamu da su ne don ya jarabcemu da su, wasu kuma don su zama alkhairi a cikin rayuwarmu.."

kasa ƙarasa maganar ya yi saboda kululun bakin cikin da ya tokare makoshin shi, ya ji zafi a ranshi, bakin ciki ya cika shi kamar zai haɗiyi zuciya ya mutu.

Kwantar da kansa ya yi saman kafaɗar Ummi, ya ɗaura hannayensa a saman bayanta.

Cikin sigar lallashi yake dan bubbuga bayan nata, tsananin tausayinta ne ya kama shi, saboda gaba daya rayuwarta a cikin jarabta ta ke, kowa dake a falon sai da ya tausaya masu, Hajiya Laila ta yi danasani, sai cizon yatsa take yi, gani take kamar hada laifinta komai ya faru, idan har Musa yana sarrafa Alhaji Ubaid da sihirinsa toh ita da hankalinta take yin komai.

A fakaice ta dinga share kwalla tana satar kallon Aisha da mahaifinta..

Cikin ruɗu Alhaji Ubaid ya ce, "Har yanzu na kasa yarda da abunda kunnuwana suke jiye min! Dan Allah ku fahimtar da ni! Kaina ya ɗaure, Wani musan kuke nufi? Ƙanina musa ko wani musan ne daban?"

Hajiya Layla ta yi saurin cewa, "Wallahi zai aika! Fiye da haka ma, ai baida mutunci ko kaɗan, mutun sai bakar zuciya kamar ta kafuran farko, na daɗe ina zargin ba mutumin kirki bane Musa, kuma dukiyarsa bata Allah da Annabi ba ce, Ai ni bazan ma Musa ba..."..

Benazir ta kar6e da cewa, "Abun da Aisha ta faɗa gaskiya ne daddy, na dade ina jiran wannan ranar da zan fadi ta cikina, ku yi hakuri da ban ta6a sanar da ku ba, na boye maku ne saboda nasan zai yi wuya ku yarda da ni a wannan lokacin, saboda ku kan ku sai yadda ya yi da ku...."

mayar da hankalinsu su ka yi akan Benazir..

A tsanake ta labarta masu komai da ya faru tun daga lokacin data ta kama shi yana yin waya agidan shi, har izuwa kan asirin da ya yi mata..

Daura hannu biyu Hajiya Layla ta yi akanta.

Mami ta zabga salati, Dr Shureim ya zabura ya mike a kidime jin ƴarsa da ya binne Uncle Musa ne ya dauke ta, yama kasa magana sai zazzare idanunsa ya ke yi gaba ɗaya ya ruɗe, nan ta ke ƙwaƙwalwarsa ta fara tariyo masa abubuwan da suka faru a baya, lokacin da ya je ya tone ƙabarinta ya ga ƙasusuwa saida ya yi zargin wani abu, just in two weeks da ya binne ta har ta zama ƙashi, bayan haka ya daɗe yana ji aranshi tana a raye saboda bai ta6a mafarki da ita a mace ba, Ya Ilahi! Yanzu ya gane komai.

Jirin tashin hankali ne ya ɗebesa yayi taga taga zai kife, Alhaji ubaid ya yi saurin miƙewa ya tallabo shi, tare da rungume shi kan kirjinshi, kukan baƙin ciki ya fashe da shi kamar ranshi zai fita, tuni zazzabi da ciwon kai sun kama shi.

Sheikh Imam ya ƙara shiga damuwa daga shi har Aisha jin rashin imanin da Uncle musa yayi ma Benazir saboda kawai ta nemi ta tona masa asiri don ta ƙwatarwa Aisha hakkin ta.

Cikin shesshekar Kuka Hajiya layla ta dinga ɗura mashi ashariya tana tsine masa albarka, dama da ƙiyayyarsa aranta, bata taɓa son shi ba, kwata kwata baya burgeta saboda izzarshi, ta tsane shi ta tsani komai nasa.

Ƙwallar bakin ciki ce ta cika idanun Alhaji Ubaid, cikin rawar murya yake ambaton duk wata addu'a da ta zo bakinsa don ya samu sassaucin radadin da zuciyar sa ke yi masa.

Abie da ke zaune a gefensa dafa kafadarsa ya yi batare da ya iya furta kalma ba, kowa ya razana da jin abun da Musa ya aika ta.

Babu wanda zuciyar sa bata karaya ba..

"Har yanzu baku fayyace mana komai ba, Ina so in san wace irin sadaukarwa ce Musa ya yi da yarinyar Shureim da kuma yarinyar Benazir? suna a raye ko sun mutu?"

Cike da fargaba Abie ya yi tambayar, saboda yana son yasan in duk a tare suke da ɗan Iya.

Shiru su ka yi saboda basu da amsar tambayar da zasu ba Abie.

_Taj Ka faɗa masu komai, yanzu lokaci ne da kowa yakamata yasan gaskiya, Illa iyaka kowa ya yi hakuri da abun da zai ji_

Zuciyarsa ce ta raya ma shi.

Gyaran murya ya yi hankalin kowa ya dawo kan shi.

falon yayi tsit kamar mutuwa ta gifta, baka jin sautin komai sai na muyar Taj dake basu labari..

Ya fara ne daga kan labarin leƙen asirin da suka yi wa matsafa shi da Uzair, rabuwarsa da Unaisah da hannun da kowan nan su ya faɗa, Alherin da Chief Owais ya yi masa da kuma haɗuwarsa da ƴarsa bayan shekaru..

Lokacin da ya fara basu labarin gidan kurkukun Ƙaddara, saida suka yi danasanin jin labarin shi, saboda matsanancin tashin hankalin da suka shiga, sun ruɗe sosai, sun razana, zuciyarsu ta tsinke da jin irin azabtarwar da ake yi wa yaran da basu ji ba basu gani ba. Babu wanda bai share ƙwalla ba acikin su, kuka ne ya kubcewa Benazir da Anila kamar ransu zai fita, Hatta Hajiya Layla da Mami saida suka yi kuka na fitar hayyaci, shi Alhaji Ubaid ma kukan zuciya mai radadi ya kama yi, shi da Abie, musamman da ya zo kan labarin Unaizah abin ya taɓa zuciyoyin su.

Jin abun suke kamar ba a gaske ya ke faruwa ba saboda ruɗun da suka shiga.

Bayan ya ƙarasa basu labarin, ya juya ya nufi sitting room din Chief ya ɗauko diary din Unaizah wanda tun shekaran jiya da ya shiga ɗakin ya gan shi akan table.

Bayan da ya dawo hannunsa ruƙe da diary din, ya Miƙa masu ya ce yana so kowan nan su ya dubi hotunan dake a cikin diary din da kyau.

Alhaji Ubaid ya fara mika mawa hannunsa na kerma ya karɓa tare da bude shafin farko, wata zabura ya yi ya mike a firgice yake tambayar diary din wanene? Mai ya kawo hoton Musa da na ƴarsa Zeenatu a cikinsa.." Da jin wannan maganar yasa Benazir ta mike cike da rashin kuzari ta nufe shi, hajiya Layla ma tuni ta mike tana leƙa hoton ta furta, "Kai! Ai Zeenatu ce wannan! Da Musan! Me ya kawo hotunansu anan? Wace ce kuma wannan baturiyar?" Ta tambaya a ruɗe.

Kowa sai da ya duba hotunan, bayan da suka gama kallo, Taj ya fayyace